TAFARKIN TSIRA
RUBUTA LABARI
MANSUR USMAN SUFI
SARKIN MARUBUTAN YAƘI
Wthapp number
08137237071

Babi na ɗaya

A wani zamani can baya mai tsawo daya shuɗe an yi wani birni a yankin ƙasashen larabawa mai suna ZAINUL ANSAR.

Birnin zainul-Ansar ya tara manyan kabilu iri daban -daban suna da arzikin noma, kiwo da tattalin arziki,
Duk da kasancewar su mabanbanta ra'ayi amma suna zaune lafiya babu tashe-tashen hankula.

Wannan ya samo asali ne saboda bisa kyakkyawan shugabanci da sarkin birnin ke zartar wa, wannan sarki ana kiransa da suna nu'umanu.

Sarki Nu'umanu yakasan ce mashahurin sadauki kuma JARUMIN JARUMAI kuma masani a fagen ilimin addinin musulunci,
A rayuwar Sarki Nu,umanu babu abinda ya ke dugunzuma hankalin shi sama da abu biyu,
Na farko shi ne rashin Haihuwar matar shi mai suna lawisat, Tun suna saurayi da budurwa su ka yi aure amma har girma ya fara kama su basu samu haihuwa ba.

A bu na biyu shine akwai wata ƙasa ta kafurai dake makwabtaka dasu suna da mu'amala mai karfi ta zaman amana atsakanin su,
Tun zamanin mahaifin sarki nu'umanu yake ta ƙoƙarin ya ga cewa sun ƙarbi musulunci amma har ya mutu basu daina bautar gumaka ba,
Hawan Sarki Nu'umanu ne ya yi tunanin cewa zai nemi duk hanyar da ya kamata domin ya ga cewa sun ƙarbi musulunci koda kuwa yaƙi zai faru tsakanin su.

Bisa wannan dalili ne yasanya ya tara dukkanin yan majalissar shi domin tattaunawa bisa wannan al'amari.

Ko da sarki Nu'umanu ya ga cewa dukkanin 'yan majalissar shi sun hallara a ɗakin taron kuma shiru ya wanzu sai ya miƙe tsaye ya yi gyaran murya a karo na farko bayan ya gabatar da salati ga Manzon Allah (s.a.w)
Kana daga bisani ya cigaba da cewa "Ya ku 'yan majalissa ku yi sani cewa bakomai ne yasanya na tara ku a nan ba sai domin mu tattauna game da al'amarin Sarki Rakibu,
Sanin kanku ne cewa mahaifin sarki Rakibu amini ne a wajen mahaifina, Abbana ya yi ƙoƙari domin ya ga cewa sarki Zaidur ya karbi addinin musulunci amma hakan ya faskara akwana a tashi yanzu ni ne a bisa KARAGAR MULKI shin yanzu haka zamu zuba idanu ana bauta wanin Allah SWT?.

Sa'adda sarki Nu'umanu ya zo nan azancen shi sai daƙin taron ya yi shiru a karo biyu,
Tsawon daƙiƙa ashirin babu wanda ya ce uffan daga bisani waziri Yazid ya yi gyaran murya a karo na farko ya ce "Allah ya taimaki sarki ina ganin ba ya cikin tsarin addini da koyarwar magabata a tilas mutum shiga musulunci face shi da kan shi ya ga Yakamata ya shiga,
Ina ganin kyauta ta mu'amalar mu da su shi n zai sake zaburo da zuciyar su zuwa ga addinin Allah SWT.

Sa'adda waziri ya zo nan a jawabin shi sai zuciyar sarki Nu'umanu ta harzuƙa ainun Amma sai ya bar abin a ran shi, ko da cewar maganar waziri ta na kan TURBAR GASKIYA,

Sarkin fada wanda ake kira da kizalu shine ya miƙe tsaye ya yi gyaran murya ya ce "Ya shugabana ina ganin abin da ya kamata a yi shi ne a tura wasiƙa zuwa ga sarki Rakibu a kwaɗaita ma shi musulunci da irin garaɓasar da zai samu idan ya shiga tare da jama'a shi, Tun da tsakanin mu da shi akwai fahimtar juna matuƙa da wahala ya yi watsi da tayin da muka yi ma shi,

Duba da cewa mun zame ma shi tamkar garkuwa, kuma mune karfin tattalin arzikin su baki ɗaya daga mu ne suke samun ingantaccen tsaro, kayan masarufi".

Lokacin da sarkin fada kizalu ya zo nan a jawabin shi sai sarki Nu'umanu ya cika da matuƙar farin ciki domin yana da tabbacin kizalu ya kawo shawara mai kyau.

Shugaban baitul-mali ne ya miƙe tsaye ya fara magana a karo na farko tun shigowar shi ɗakin taron ya ce "Allah ya taimaki waziri ya shugabana kada ka manta cewa tsawon shekaru muna kyauta ta mu'amalar mu da mutanen sarki Rakibu amma ga shi ɗayan su bai shiga addinin Musulunci ba ina ganin shawarar sarkin fada ita ce mafita, idan ma har suka karɓi karɓar tayin da muka yi masu a cikin wasiƙar za mu yanke duk wata hulɗar kasuwanci tsakanin mu, wannan shi ne ra'ayi na Allah ya taimaki waziri".

Sa'adda shugaban baitul-mali ya zo nan a zancen shi sai ɗakin taron ya sake yin shiru a karo na uku,

A wannan lokaci sai da aka shafe tsawon lokaci babu wanda ya ce uffan.

Ko da ganin hakan sai sarki Nu'umanu ya yi gyaran murya a karo na biyu ya ce " Na ji dukkan shawarwarin ku yanzu abin da ya dace shi ne za mu sake taro a nan a mako mai zuwa domin na yi nazari akan hakan na bar ku lafiya wassalam".

Ko da sarki nan a zancen shi sai ya miƙe tsaye ya ci wata 'yar siririyar hanya da ke da zata sada shi da gidan sarauta waɗansu ZARATAN DAKARU masu jajayen tufafi suka mara ma shi baya, take ɗakin taron ya watse kowa ya kama gaban shi.

## BABI NA BIYU

Ayarin fatake ne da adadin su ya kai ɗari tara da ɗoriya, tafiya suke wasu akan dawakai, raƙumi, wasu a ƙafa, su dai wannan ayari ana iya kiran su da 'yan GUDUN TSIRA, domin kuwa kallo ɗaya za ka yi masu ka fahimci hakan dalilin yara, mata da tsofaffi

Ayarin suna tafiya ne a cikin dokar daji ma'abocin dogayen bishiyu, duwatsu da kwazazzabai, Hakan ne ya sanya duhu ya mamaye dajin, sai da ayarin suka iso tsakiyar dajin kwatsam! bazato babu tsammani sai aka ga waɗansu ZARATAN MAYAKA suna yin fitar bdaga cikin duhuwar bishiyun dajin suna yi masu ƙawanya,

Ko da bayyanar dakarun sai kawai suka ce da wa Allah ya haɗamu sai suka afkawa ayarin da azababban yaƙi, nan take waje ya kaure da koke-koken yara ƙanana, mata da tsofaffi.

Abin tambaya a nan shi ne daga ina waɗannan ayari suke? Kuma ina suka nufa?.

Su dai ayarin sun fito ne daga wata ƙaramar alkarya da ake kira da kira da suna Baitul-Hazwar.

Birnin Baitul-Hazwar ya bunƙasa a noma, kiwo da kasuwanci, dadin daɗawa kuma sun tara MAZAN JIYA masu juriya a filin fama,

Sarkin dake riƙe da kambun Sarautar birnin ana yi masa lakabi da Hidayal,
Sarki Hidayal yakasance dattijo ma'abocin kwarjini da haiba shekarun sun haura hamsin alamun tsufa sun fara riskar shi amma duk da hakan ya kasance gwarzon mayaƙi kuma JARUMIN JARUMAI,
A rayuwar Sarki Hidyal babu abin da ya tsana fiye da zalunci da cin zarafi bisa wannan dalili ya sanya ya ke gudanar da mulkin shi bisa adalci,
Al'amarin da ya janyo ma shi daraja da ƙima a idanun sarakunan dake makwabtaka da shi kenan suke ɗaukar shi a matsayin ubansu, kuma suka ƙulla hulɗar kasuwanci tsakanin su da shi, al'amarin da ya sanya tattalin arzikin birnin shi ke bunƙasa kenan da sauran biranen.

A rayuwar Hidyal babu abin da ya ke ƙauna kamar 'ya'yanshi yarima Usaib da gimbiya Haifar,
Usaib da Hairat sun kasance kyawawa na gaban kwatance, tun suna da shekara biyar a duniya suke nuna abubuwan al'ajabi,
Lokuta da yawa idan sarki ya fito rangadi tare da su idan gungun 'yan fashi da makami suka gan su sai kaga sun tarwatse zuwa cikin daji sun cika wandonsu da iska, idan kuwa muguwar dabbar daji ta haɗa idanu da su Usaib sai ka ga ta sunkuyar da kanta ƙasa cikin ladabi ta juya ta shige zuwa cikin daji.

Lokacin da usaib da 'yar uwar shi Hairat suka cika shekaru goma da haihuwa sai suka rinƙa shiga cikin daji suna farauto namun daji irin su zaki, ƙura, damisa da sauran su, wani abu da yafi ɗaurewa mutane kai shi ne koda zabirar aski ba su taɓa riƙe wa ba ballantana su fita yaƙi,
Akwai wata rana da wani hatsabibin dodo ya bayyana a birnin domin ya hallaka duk wata halitta da ke ciki, har dakarun yaƙi sun fita da nufin su afkawa dodon kawai sai aka hango su yarima Usaib sun fito daga dajin birnin sun tunkaro inda dodon yake,
Cikin matuƙar kaɗuwa sarki Hidayal ya zaburo dokin shi ya tunkari inda suke yana mai ƙwala masu kira yana cewa "Ya 'ya'yana kada ku iso inda wannan dodon yake.

Al'amarin dodon kuwa sa'adda ya ji takun sawaye a bayan shi sai ya waiga domin ya ga ko mene ne aikuwa koda ya yi arba da su Usaib sai a ka ga ya durƙusa ƙasa bisa gwiwoyin shi cikin ladabi.

Usaiba ya taka da ƙafafuwanshi har zuwa inda dodon yake ya dafa kanshi, kawai sai aka ga dodon ya miƙe tsaye ya ruga izuwa cikin daji ya ɓace ɓat tamkar bai taɓa wanzuwa ba,
Nan fa jama'a suka cika da matuƙar mamaki da murna suka ɗauki Usaib da Hairat suka shiga da su cikin birnin suna masu kirari da jinjina sun masu cewa tabbas sarki Hidayal ya haifi yara 'yan baiwa,
Nan fa labari ya watsu a birnin Baitul-Hazwar da ƙasashen da ke nahiyar akan abubuwan al'ajabi da su Usaib ke bayyanawa,
Wasu ma suna cewa anya kuwa waɗannan yara bil'adama ne?.

Bayan mako guda da faruwar wannan al'amari da la'asar sakaliya jama'a na gudanar da aiyukan su cikin annashiwa da jin daɗi, sarki na zaune a fadarshi ana gudanar da sha'anin mulki kamar yadda aka saba,
Kwatsam! bazato babu tsammani sai aka ji gari ya kaure da guje-guje gami da ifice-ificen jama'a cikin hanzari aka buga kugen yaƙi, dakaru suka dinga kwaso makaman yaƙi suna rugawa izuwa bakin ƙofar gari domin tarar abokan gaba, har wandu Barada sun yunƙura da nufin su buɗe ƙofar birnin sai kawai aka ga ƙofar ta karye, Kafin ayi wani yunƙuri ta danne dakaru masu tarin yawa sun sheƙa barzahu.

A lokacinne dakarun birnin Baitul-Hazwar suka yi arba da wata irin ƙasaitacciyar rundunar MAYAƘA, Nan fa suka firgice suka ɗimauce,
Ba komai ne ya firgita su ba sai bisa ganin tsananin kwarjinin rundunar nan fa su ka ji tamkar su koma da baya,
Ita dai rundunar ta kasance mai matuƙar yawa idan mutum ya kalle ta sai ya ga tamkar sun tokare da gajimare saboda matuƙar yawansu, makaman yaƙin su kuwa gasu nan birjik bila-adadin, wasu suna zaune a bisa dawakai, raƙuma, toron giwa har da dabbar da idanu ba su taɓa gani ba,
Kaico! haƙiƙa komai dakewar zuciyar jarumi idan ya yi arba da rundunar dole ya ɗimauce.
Ana cikin wannan hali ne aka hango sarki Hidyal tare da muƙarraban shi sun tunkaro wajen zaune bisa dawakai shirye cikin gagarumar shigar yaƙi mai matuƙar kwarjini da ban tsoro zaune bisa dawakai ɗauke da malamai,
Yayin da ya iso ne ya ga halin da jama'ar shi ne ciki sai buɗe baki cikin murya mai ƙarfafa gwiwa ya ce "Ya ku jama'ata ku yi sani cewa wannan yaƙi mun fito shi ne domin kare rayukan iyalanmu, duniyoyi gami da martani birninmu domin haka babu gudu babu ja da baya".
Ko da gama faɗin wannan jawabi sai sarki Hidyal ya zare takobinshi ya ɗaga sama ya zaburi dokinshi ya ruga zuwa kan abokan gaba,
Take dakarun shi suka yi koyi da shi suna ihu da kururuwa mai firgitarwa aka afkawa abokan gaba.
Nan take waje ya kaure da ƙarar karafniyar ƙarafa gami ihun Mazaje, ƙura ta turnuƙe sararin samaniya tamkar dare ya kawo kai, Sassan jikkunan bil'adama suka dinga shawagi a sararin samaniya suna zubowa ƙasa, dawakai suka dinga dudufniya kofatunsu na kartar ƙasa suna tayar da ƙura, jini ya na kwaranya, tsartuwa yana malala a ƙasa tamkar an buɗe kan fanfo,
Sai da aka shafe tsawon sa'a ɗaya ana wannan ƙazamin artabu babu sassauci yazamana cewa rundunar abokan gaba sun hallaka kaso huɗu bisa shida na dakarun birnin Baitul-Hazwar,
Sa'adda yazamana sa'a biyar ta shuɗe a dai-dai wannan lokaci ne abokan gaba suka hallaka baki ɗaya sarki Hidyal da dakarun shi babu ɗaya da ya tsira da rayuwar shi.
Ko da samun wannan gagarumar nasara ne sai wani kyakkyawan saurayi daga cikin abokan gaba ya zira hannunshi a aljihun shi na riga ya ɗauko madubin tsafin shi ya shafe shi da hannunshi na hagu ya shiga gudanar da bincike,
Jim kaɗan bayan kammala hakan sai ya juya ya dubi wani barde dake tsaye a hannun shi na dama cikin kaɗuwa ya ce da shi "Yakai Huzlan haƙiƙa binciken da na gudanar a yanzu ya tabbatar mani da cewa a lokacin da muke fafata yaƙi da jama'ar birnin Waɗansu a cikin su sun yi gudun hijira,
Domin haka wajibi mu bazama domin nemo yaro mai hatimin takobin saiful-zayyada ina so ka haɗa da dakaru mutum dubu ashirin,
Ko da jin wannan batu daga bakin Saurayin sai Barde Huzlan ya yi wa wasu dakaru inkiya ta wutsiya idanu, take su ka shiga yin wani sahu na musamman a bayan shi suna fuskantar wani ɓangare,
Kawai sai wannan kyakkyawar saurayi ya zaburi dokinshi ya nausa zuwa cikin daji take Barde Huzlan da dakarun dubu ashirin suka mara mashi baya,
Take sauran tawagar abokan gabar suka shiga kwashe gawarwakin 'yan uwan su, bayan sun kammala suka nausa zuwa wata hanya ta daban a dajin suna tsala azababban gudu a bisa dawakan su.

Kaico!  inda  mutum yana tsaye a wannan lokaci zai ga yadda gawarwakin yara da mata da mazaje ke kwance cikin jini dole tausayi ya kama shi ya zubar da hawayen baƙin ciki, kuma ya tabbatar da cewa haƙiƙa yaƙi shi ne mafakar dukkan wata musiba a doron ƙasa.
Wannan shi ne dalilin da yasanya waɗannan ayarin 'yan gudun hijira ke yin gudun tsira a cikin wannan daji.

Lokacin da wannan runduna ƙarƙashin jagorancin Sadauki Hukaiza suka afkawa ayarin fataken da azababban yaƙi, sai jini ya dinga kwaranya tamkar an ɓalle teku, rayuka suka dinga rabuwa da gangar jiki suna shawagi a sararin samaniya suna zubowa ƙasa tamkar ana ruwan su ne daga saman, ƙarar karafniyar ƙarafa gami ihun Mazaje ta cika dodon kunne.
Kaico! Nan fa dakarun suka shiga hallaka rayukan su babu wanda suke tausaya wa tsakanin yara da mata,
Inda ace mutum ya ba tsaye a wannan waje lokacin da dakarun ke aiwatar da wannan rashin imani dole ne tausayi ya kama shi ya zubar da hawaye.
Kafin shuɗewar daƙiƙa ɗari huɗu sun hallaka baki ɗaya ayarin sun zubar da gawarwakin su ƙwance cikin jini babu kyawun gani.
Bayan ƙura ta lafa ne Waɗansu ZARATAN MAYAKA suka shiga bincike gawarwakin domin su gano yaro mai hatimin takobin Saiful-zayyad a gadon bayanshi.
Jim kaɗan bayan sun kammala sai suka tabbatarwa da shugaban su cewa babu yaro mai hatimin takobin Saiful-zayyad a cikin gawarwakin,
Ko da shugaban ya ji wannan batu sai hankalinshi ya dugunzuma ainun ya dubi dakarun cikin matuƙar damuwa ya ce "Ya ku 'yan uwana dakaru sanin kanku ne cewa mai girma Lamsarul-Azlam bai tura mu hallaka ayarin 'yan gudun hijirar ba sai domin mu hallaka yaro mai hatimin takobin Saiful-zayyad, kuma ya faɗa mana cewa yaron yana cikin birnin Baitul-Hazwar, To kenan hakan ya tabbatar da cewa lokacin da muka tare waɗannan ayari ke nan yaron ya yi gudun tsira,
Ina so ku sani cewa farautar yaron shi ne zai sanya dukkan ruhikan mu su kuɓuta daga TSANANI DA UKUBA ta mai girma Lamsarul-Azlam.
Ko da shugaban ya zo nan azancen shi sai dakarun suka kasu gida biyu, na farko su ka yi yamma bisa jagorancin Sadauki Hukaiza, na biyu bisa jagorancin Barde Huzlan, suka sukwani dawakan su izuwa cikin daji.

## BABI NA UKU

Gidan sarautar ya yi matuƙar ƙawatuwa da nau'ikan abubuwan jin daɗin rayuwar duniya har da ma abin da idanu ba su taɓa gani ba,
Duk ƙasaitar BASARAKE ko attajiri idan ya tsinci kanshi a cikin wannan gida dole ne ya raina kanshi ya tabbatar da cewa GABA DA GABANTA,
Idan mai kallo ya yi duba ga wani ɓangare a gidan zai yi arba da wata turaka da ta ƙawatu ainun da kayan ado fiye da ko wane waje a gidan.
Idan mai kallo ya ƙara nazari sosai zai yi arba da waɗansu ƙayatattun kujeru zaune a bisa kan su waɗansu ZARATAN JARUMAI ma'abota mulki sanye cikin ƙayatattun tufafi suna masu fuskantar juna shiru ne ya wanzu tsakanin su na wani lokaci.

Daga can sai waziri Yazid ya yi gyaran murya ya fara magana a karo na farko ta hanyar buɗe baki ya yi gyaran murya ya ce " Ya kai Rakibu ka yi sani cewa bakomai ya sanya na kawo maka wannan ziyara ba face saboda na sanar da kai wani al'amari da yake shirin faruwa gare ka, wanda idan har baka bani goyon baya zaka rasa sarautar ka da jama'ar ka baki ɗaya".

Cikin alamun rashin fahimta sarki Rakibu ya dubi waziri ya ce "Ya amintacen waziri ga Sarkin Musulimci Nu'umanu ibnu Abbas shin wane mummunan al'amari ne ke shirin faruwa gare ni? Ina so ka gaggauta sanar da ni domin samun mafita".

Ya ƙare furucin na shi hankalin shi a tashe.

Ko da jin wannan batu sai waziri ya bushe da dariyar mugunta sai da ya yi dariyar ta ishe shi sannan ya tsuke bakin shi, kawai sai ya tunatar ldanuwanshi ya shiga karanta ɗalasiman tsafi, a lokaci guda ya tsuke bakinshi tare da yin nuni da hannunshi na hagu ga bangon turakar.

Al'amarin da ya yi matuƙar ɗaurewa Sarki Rakibu kai kenan kuma ya ba shi mamaki bisa jin waziri ya na karanta ɗalasiman tsafi a matsayin shi na musulmi wanda aikata fita daga addinin Musulunci ne baki ɗaya.

Ko da waziri ya ɗauke hannun shi daga bangon sai taswirar ɗakin taro ya bayyana, Nan take Rakibu ya ga dukkan tattaunawar da sarki Nu'umanu ya yi da 'yan majalissar shi tun daga farko har ƙarshe, Sannan waziri ya sake nuna bangon a karo na biyu taswirar ta ɗauke tamkar bai taɓa wanzuwa ba.

Sa'adda Sarki Rakibu ya ga Wannan taswirar sai hankalinshi ya dugunzuma ainun fiye da ko yaushe.

Waziri Yazid ya yi gyaran murya a karo na biyu ya ce " Ya kai Rakibu ka yi sani cewa wannan tattaunawar an yi ta ne domin a juyar da al'ada da addinin ku da ku ka gada tun iyaye da kakanni, kuma ina mai tabbatar maka da cewa dole a kwabza yaƙi tsakanin mu da kai,
Sanin kanka ne cewa ko ba a gwada ba linzami yafi ƙarfin bakin kaza, ko na ce SARKIN YAWA yafi SARKIN KARFI, ma'ana dakarun mu ba sa'anni ba ne da na ka,
Na sani cewa a halin yanzu hankali ya shiga tararrabi da ɗimauta amma idan har zaka haɗa kai da ni za mu samu nasarar murƙushe Sarki Nu'umanu daga kan KARAGAR MULKI,
Da yake masu iya magana na cewa "Da ɗangari akan ci gari" to mu haɗa ƙarfi da ƙarfe da sarkin yaƙi lauzar tare da waɗansu fitattun MAYAKA na birnin Baitul-Hazwar,
Kawai za mu afkawa birnin ne da rana tsaka domin mu ci su da yaƙi da zarar mun samu nasara zan ɗare bisa KARAGAR MULKI ta sarki Nu'umanu, sarkin yaƙi lauzar zai cigaba da riƙe muƙamin waziri, kai da jama'ar ka kuma za ku cigaba da tafiyar al'ada da addinin ku batare da wata matsala ba".

Ko da jin wannan dogon bayani bakin waziri sai hankalin sarki Rakibu ya ɗugunzuma ainun fiye da Kowa ne lokaci ya ji tamkar ya kurma ihu cikin ƙankanin lokaci zufa ta fara tsattsafo mashi,
Ya shiga juya al'amarin a cikin ran shi ya ƙulla wannan ya warware wancan.

Abu na farko da ya dugunzuma hankalin shi ne ya tabbatar da cewa idan ya fafata yaƙi da sarki Nu'umanu ba zai taɓa samun nasara ba domin idanu ba nufi ba ne amma sun kima"
Abu na biyu shi ne yanzu zai karɓi addinin Musulunci ne wanda tabbas shi ne addinin gaskiya da ke bisa TAFARKIN TSIRA, haƙiƙa yin hakan zai tserar da sarki Nu'umanu daga mugun tanadi da ɓakin makircin waziri Yazid,
Shin yanzu ta ya ya zan ƙyale addini na da na gada tun iyaye da kakanni tabbas wannan babban abin kunya ne a gare ni.

Haka dai Rakibu ya dinga nazari akan al'amuran har daga ƙarshe ya yanke shawarar ya yi biyayya ga waziri Yazid domin ba zai taɓa barin turbar shi ta gado ba wacce ya tabbatar da cewa bakomai ba ce face TURBAR AJALI.

Rakibu ya tattara hankalin shi ga waziri ya dube shi ya ce "Ya kai Yazid haƙiƙa tabbas na amince da shawarar ka yanzu batare da ɓata lokaci ba a cikin dare kafin ketowar alfijir zai kammala haɗa rundunar MAYAƘA na".

Da jin wannan batu sai waziri Yazid ya cika da matuƙar farin ciki maral-musaltuwa domin yana ganin cewa yana kusa da cika burin shi na ɗarewa bisa KARAGAR MULKI ta birnin Zainul-Ansar.

Gudu suke yi tamkar diga-digansu za su karairaye saboda matsanancin gudun tsira da rayukansu.

Ƙananan yara ne mace da namiji da shekarun su ba zasu haura goma da haihuwa ba,
Suna gudun ne a cikin wani ƙasaitaccen daji ma'abocin dogayen bishiyu, duwatsu da ƙoramu,
Suna cikin gudun ne kwatsam bazato babu tsammani sai suka ga wani murgujejen zaki ya yi fitar burgu daga duhuwar bishiyun dajin ya bayyana a gare su yana gurnani da ɗaga ƙafafuwanshi sama, kawai sai suka ja suka tsaya cak! tamkar waɗansu gumaka dukkanin su sun sallama cewa a halin yanzu rayuwar ta zo ƙarshe,
Lokacin da ya rage saura taku uku zakin ya cimma su kwatsam sai kawai suka ga ya yi sama tamkar an janye shi da ƙugiya sannan daga bisani ya faɗo ƙasa tim a matuƙar galabaice, kafin ya yi yunƙurin miƙe tsaye ta dunƙuke hannayen ta biyu ta gabza ma shi naushi a wuya take ya karye jikake ruƙus! Ƙas ya faɗi ƙasa matacce ko shurawa bai yi ba,
Cike da matuƙar mamaki suka ƙura mata idanu suna al'ajabin irin sadaukantakar ta da kuma ƙoƙarin ceto rayuwar su da ta yi,
Ita kuma ta na mamaki bisa ganin su a cikin wannan mugun daji mai cike da haɗari a matsayin su na yara ƙanana da ya kamata ace suna zaune a gaban mahaifansu.

Suna cikin wannan hali ne rundunar sarki Lamsarul-Azlam ta tunkaro wajen a sukwane bisa dawakai,
Sa'adda yaran biyu suka arba da su nan take suka fara zubar da hawaye,
Al'amarin da ya sanya wacce ta ceci rayuwar ta su ta fahimci cewa dakarun ne suke yunƙurin cutar da su saboda haka ne suka shigo cikin dajin yin gudun tsira,
Ko da fahimtar hakan sai kawai ta tuntse idanuwnta ta karanta waɗansu ɗalasiman tsafi, tana gama rufe bakinta take ta ɓace ɓat tare da yaron tamkar ba su taɓa wanzu ba.

Cikin matuƙar takaici da baƙin ciki shugaba Hukaiza da sauran dakarun suka ja linzamin dawakan su suka tsaya cak,
Kawai sai Hukaiza ya ɗauko madubin tsafin shi ya shafe shi da hannunshi na hagu da nufin gudanar da bincike amma sai kawai ya ji an ja shi sama daga kan dokinshi an fyaɗa shi da ƙasa,
Al'amarin da ya yi matuƙar dugunzuma hankulan dakarun kenan domin tun da suke da shugaban na su hakan bai taɓa faruwa ba.

BABI NA HUƊU

Tun sa'adda sarki Nu'umanu ya baro ɗakin tattaunawa da 'yan majalissar shi sai ya kasa zaune ya kasa tsaye ya wanzu yana kai komo a cikin turakarshi ya saƙa wannan ya kunce wannan,
Tsawon daƙiƙa hamsin yana nazarin shawarar 'yan majalissar a cikin ran shi,
Inda daga bisani dai ya yanke shawarar ya yi amfani da maganar magatakarda na aikawa sarki Rakibu da WASIKAR gayyata zuwa addinin Musulunci.
Ko da gama yanke shawarar sai kawai ya fice daga turakar domin zuwa masallaci
Waɗansu ZARATAN MAYAƘA suka mara mashi baya, duk inda ya huce a gidan sarautar sai dai kaga dakaru, hadimai, barori, kuyangi da bayi na zubewa ƙasa suna kwasar gaisuwa a haka har ya iso zuwa masallacin dake wajen gidan sarauta.
Wannan shi ne abin da ya faru da sarki Nu'umanu na birnin Zainul-Ansar.
Al'amarin waziri Yazid kuwa, bayan sarki Rakibu ya aminta da shawarar da ya zo masa da ita kuma ya ɓace cikin alƙalumman sihiri,
Domin zuwa birnin Zainul-Ansar bai bayyana a ko ina ba sai a cikin sai a cikin turakarshi,
Turakar ta ƙawatu ainun da nau'ikan kayan ƙawa da alatun jin daɗin rayuwar duniya har da abin da idanu ba su taɓa gani ba,
Batare wani jinkiri ba ya tura wata kuyangar shi izuwa gidan Sarkin yaƙi lauzar da wasiƙa mai ɗauke da dukkan tattaunawar da suka yi da sarki Rakibu da kuma shirye-shiryen da zasu gudanar,
Sarkin yaƙi ya yi matuƙar farin ciki da samun wannan sako,
Don haka cikin hanzari ya shiga tara rundunar MAYAƘA su kimanin dubu goma cikin sirri suka nufi daga ɓoyayyar hanyar suka fice daga birnin domin saduwa da inda dakarun sarki Rakibu suke batare da wani ya gane su ba.

TAFARKIN TSIRA
Rubuta Labari
MANSUR USMAN SUFI
SARKIN MARUBUTAN YAƘI
Wthapp Number
08137237071

BABI NA BIYR

Boka kaddad ya dubi aljani Lattul-kifas ya ce da shi " Ya kai Lattul-kifas ka yi sani cewa bakomai ne ya sanya na kira ko nan ba sai domin ina so ka tafi gabas maso arewacin duniya ka ɗauko Mani wani yaro mai ɗauke da hatimin takobin Saiful-zayyad a gadon bayanshi".
Ko da jin wannan batu sai Lattul-kifas ya buɗe baki cikin ladabi cikin wata irin kakkausar murya mai kama da saukar aradu ya ce "An gama ya shugabana wannan aiki ai cire silin gashi

daga cikin tandun mai ya fi shi wahala a waje na, amma kafin haka ya shugabana ina da tambaya shin mene ne ya sanya ake kiran takobin da suna Saiful-zayyad?.

Boka kaddad ya murtuke fuska ya ce "Ai Wannan tambaya ta ka bayani mai zurfi wanda ko da zamu kwana ɗari ina baka ba zai yiwu mu zo ƙarshen shi ba,

Amma a jawabi a takaice anan shi ne

Sadauki zayyad wani gawutaccen mayaƙi ne da a ka yi wanda bokaye da masu hasashe suka tabbatar da cewa a wannan ƘARSHEN ƘARNI babu gwarzon mayaƙi tamkar shi tsakanin duniyar MUTUM DA ALJAN a wannan lokaci ya zame wa sarakunan duniya da bokaye ANNOBA ƊARI, ko da sunan shi aka ambata sai ka ga boka ya ɗimauce saboda matuƙar tsoro,

Asalin Sadauki zayyad yakasance mutum birnin biladul-tukrur dake yammacin duniya

Kuma yakasance ma'abocin wani addini da ake yiwa lakabi da musulunci.

Kawai dai yanzu abin da nake so ka sani shi ne mallako wannan yaro shi ne zai kawo kwanciyar hankali a wannan duniya ta bil'adama, sabanin hakan kuwa na iya haddasa ɓarkewar ANNOBA ƊARI.

Sa'adda Aljani Lattul-kifas ya ji wannan batu daga mai gidan shi sai ya risina ya ce "An gama ya shugabana",

Yana gama faɗin hakan ya juya ya kaɗa manyan FukaFukanshi ya tashi zuwa sararin samaniya ya ɓace ɓat a cikin gijimare.

Bakomai ne ya sanya boka Kaddad ya ke so a farauto mashi yaro mai hatimin takobin Saiful-zayyad ba, sai domin bisa binciken da ya gudanar halarar tsafin shi ta tabbatar nashi da cewa matsawar yana so yafi kowa ne bil'adama ƙarfin damtse da sihirin tsafi sai ya yanka yaro mai hatimin takobin ya shanye jinin shi,

Bisa dalilin hakan ne ya umarci aljani Lattul-kifas ya ɗauko yaron.

BABI NA SHIDA

Al'amarin wannan baƙuwar jaruma kuwa tun sa'adda da ta ɓace cikin alƙalumman sihiri tare da ƙananan yara biyu bayan ta ceci rayukan su daga hannun dakarun Sarki Lamsarul-Azlam,

Ba su bayyana a ko ina ba sai a cikin wata ƙasaitacciyar turaka da aka ƙawata ta da nau'ikan kayan alatu daban-daban, komai ƙasaitar BASARAKE ko attajiri idan ya tsinci kanshi a cikin wannan turaka dole ya raina kanshi ya tabbatar da cewa GABA DA GABANTA aljani ya taka wuta.

Masana tarihin duniya da masu hasashe na wannan SABON ƘARNI sun tabbatar da cewa a wannan zamani babu wani attajiri fiye da mai mallakin wannan gida, wato shugaban 'yan fashin duniya Sadauki Fitinatul-Amir,

An ambace shi da Fitinatul-Amir ne saboda ya zamowa sarakunan duniya ƙadangaren bakin tulu kuma ciwon idanu,

Amma asalin sunan shi shi ne Huraisu ibn Dazwan.

Huraisu yakasance MASHAHURIN SADAUKI mai tarwatsa DANDAZON MAYAƘA a filin fama, Gawutaccen matsafi ne kuma fitaccen ɗan fashi da makami da ya zamowa duniya ANNOBA ƊARI,

Bincike ya tabbatar da cewa a kaf sarakunan bil'adama babu attajiri tamkar shi haɗe da ilimin tsafi,

Wanda yake kunnen doki da su a fagen sihiri su ne Sarkin dake mulkin bakaken aljanu sarki Sulusainul-layal tare da sarki Lamsarul-Azlam na birnin Darul-Ashmar.

Duk sarkin da Sarkin 'yan fashin duniya ya sanya a gaba sai ya ga bayan shi komai irin matuƙar yawan rundunar mayaƙan shi da dukiyar shi,
Bisa wannan dalili yasanya sarakunan duniya ke aika mashi da harajin mai tarin yawa a kowace shekara domin ganin sun tsira da rayukansu da biranensu.
Ta wannan hanya ne Fitinatul-Amir ya tara dukiya mai yawan da babu kamar ta,
Sai dai duk tarin dukiyar shi da ya tara ta tashi a banza domin ba shi da magaji da zai zamo halifan shi bayan rasuwar shi,
Duk sa'adda ya ga Wannan al'amari a cikin alƙalumman sihirin shi sai ya cika da matuƙar baƙin ciki maral-musaltuwa,
Bisa binciken da ya gudanar bisa halarar tsafin shi ya gano cewa har abada ba zai taɓa samun haihuwa ba face ya hallaka wani yaro mai hatimin takobin Saiful-zayyad a gadon bayanshi,
Domin shi ne zai kawo KARSHEN ZALUNCI shi, bisa wannan dalili ne ya sanya dare da rana Fitinatul-Amir ba shi da wani aiki face farautar yaro mai hatimin takobin,
Babban abin da ya fi dugunzuma hankalin shi shi ne, Duk sa'adda ya tsananta bincike domin ya gano inda yaron yake zaune a duniya sai madubin tsafin na shi ya yi bindiga ya tarwatse,
Amma duk da faruwar hakan bai sanya gwiwoyin shi sun yi sanyi ba wajen farautar yaron domin ya cire kan shi barcin dare kawai saboda binciken yaron a cikin alƙalumman sihiri.

***

Bayan Jarumar ta sauke waɗannan yara biyu a cikin ƙasaitacciyar turakar sai ta umarci waɗansu irin tsala-tsalan kyawawan kuyangi suka suka ɗauki yaran suka shiga da su izuwa kewaye suka yi masu wanka suka sanya masu tufafi masu tsadar gaske irin na hamshaƙan sarakai sannan suka dawo da su izuwa cikin turakar,
A sannanne baƙuwar jarumar ta shiga ba su abinci da abin sha gami da nau'ikan kayan marmari suna ci sai da suka ƙoshi suka samu nutsuwa.

"Ya ku waɗannan yara ina so ku sanar da ku labarin rayuwar ku kuma mene ne ya sanya waɗannan dakarun ke farautar ku domin su hallaka ku?.

Ko da jin wannan tambaya sai sai yaran suka fashe da matsanancin kuka mai tsuma zuciya daban tausayi,
Al'amarin da ya yi matuƙar bawa Rusayyat mamaki kenan kuma ya sanya ta kamu da matuƙar tausayin su ta janyo su ta rungume a kirjinta ta shiga rarrashin su har da suka yi shiru sannan ta janye jikinta daga na su,
A karo na farko Namijin wanda ake kira da suna Usaiba ya ce " Ya ke wannan jaruma ma'abociyar tausayi da jin ƙai ki yi sani cewa bakomai ne ya sanya mu gudun tsira da rayukanmu a cikin wannan daji ba sai domin tsira daga sharrin dakarun sarki Lamsarul-Azlam wanda ya rabu da mahaifin mu da muka fi so fiye da komai a duniya,
A lokacin da muka baro birnin mu mun kasance ayarin 'yan gudun hijira fiye da mutum dubu,
Azaton mu mun samu kuɓuta daga TSANANI DA UKUBA ashe dakarun sarki Lamsarul-Azlam suna biye da sahun mu, sai da suka tabbatar mun saki jiki a cikin daji sannan suka afka mana suka hallaka dukkan ayarin mu har ta ƙananan yara da mata ba su ƙyale ba,
A halin yanzu mu kaɗai ne mu ka rage daga cikin al'ummar birnin mu mu kan mu na domin ke ba da tuni mun daɗe da baƙuntar barzahu,

A halin yanzu rayuwar mu bata da wani amfani, domin mun rasa duk wani farin cikin rayuwar mu".

Lokacin da yaro usaiba yazo nan azancen shi sai suka sake fashewa da matsanancin kuka mai tsuma zuciya a karo na biyu,
Rusayyat bata san sa'adda hawaye suka kwaranyo daga idanuwanta ba ta sake ruguntsume su Usaiba a karo na biyu ba, tsawon daƙiƙa ashirin suna cikin wannan hali sai daga bisani ne ta yanye jikinta daga na su suka fuskanci juna a lokacin da Idanuwanta suka ciki da ƙwalla kuma suka kaɗai suka yi jajur ta dafa kafaɗunsu sannan ta buɗi baki cikin murya mai taushi da ban tausayi ta ce "Ya ku waɗannan yara ku yi sani cewa wannan na ku ya sanya ni na kamu da soyayyar ku kuma ya tuna mani da nawa labarin da nake da tabbacin ya huce na ku ban tausayi da tsantsar zalunci,
Ina so ku zauna tare da ni a wannan gida zan baku dukkan wata kulawa da uwa ke bawa 'ya'yan ta,
Ku shiga duk inda kuke so a wannan gida ku ɗauka tamkar a masarautar ku ne,
Zan baku horon yaƙi har izuwa lokacin da za ku iya ɗaukar fansa akan sarki Lamsarul-Azlam,
Ina so ku riƙe ni a matsayin tamkar mahaifiyar ku ni kuma zan riƙe ku tamkar 'ya'yan da na haifa".

Ko da Usaiba da 'yar uwar shi suka ji wannan batu daga bakin Rusayyat sai suka cika da matuƙar farin ciki maral-musaltuwa.

Usaiba ya yi gyaran murya ya ce "Ya ummina shin ko mene dalilin da sanya kika ce labarin rayuwar ki ya fi namu ban tausayi?.

Da jin wannan tambaya sai Rusayyat ta cika da matuƙar farin ciki bisa jin usaiba ya ambace ta da suna ummina, cikin matuƙar farin ciki ta dube shi ta ce "Ya farin cikin rayuwata ka yi sani cewa tabbas magana ta babu jayayya akan ta, Duk sa'adda na samu nutsuwa zan ba ku labarin domin ku tabbatar,
Yanzu abin da ya fi muhimmanci shi ne ku kwanta ku huce gajiyar da eh tare da ku,Ko da jin wannan batu sai farin ciki ya mamaye zukatansu,
Kawai sai usaiba ya koma bisa wata ƙasaitacciyar kujera ya kwanta ita kuma Hairat sai ta kishingiɗa a bisa wani ƙayataccen gado,
Ko da ganin hakan sai Rusayyat ta miƙe tsaye ta nufi Kofar fita turakar tana mai waigen su tana sakar masu ƙayataccen murmushi mai cike da tsantsar so da kauna a haka har ta fice baki ɗaya dakarun masu tsaro suka janyo ƙofar suka rufe rufe.
wannan shi ne abin da ya faru da baƙuwar jaruma da ta ceto rayuwar waɗannan yara biyu daga sharrin zaki da kuma dakarun sarki Lamsarul-Azlam, wato jaruma Rusayyat uwar gidan shugaban 'yan fashin duniya Sadauki Fitinatul-Amir.

TAFARKIN TSIRA 4
Rubuta Labari
MANSUR USMAN SUFI
Sarkin Marubutan Yaki
Wthapp Number
08137237071

BABI NA BAKWAI

sa'adda waziri Yazid, sarkin yaƙi lauzar da sarki Rakibu suka kammala shirya rundunar MAYAƘAn su sai da suka bari dare ya tsala sannan suka durfafi hanyar da zata kai su zuwa birnin Zainul-Ansar.

Tafiyar rabin sa'a kacal suka yi suka iso domin haka sai suka yiwa birnin ƙawanya,

Waziri Yazid ya yi gyaran murya ya ce "Ya ku dakarun haɗin gwiwa ku yi sani cewa yaƙin ku da dakarune kawai ba jama'ar gari ba da kuma duk wanda ya yi yunkurin kawo maku tazgaro domin ku isa zuwa turakar sarki Nu'umanu,

Yana zuwa nan a zancen shi sai ya umarci masu kibbau suka ɗana bakansu sannan suka harba shi izuwa dakarun dake tsaron ƙofa,

Sannan suka afkawa birnin suka hau dakaru da sara da suka, ihun Mazaje da kururuwar su shi ne abin da ya fara sauka akan kunnuwan jama'ar birnin.

Nan fa aka ruguntsume da azababban yaƙi mai matuƙar kwarjini da ban tsoro,

Ɓangarorin biyu suka wanzu suna kaiwa juna sara da suka cikin matuƙar zafin nama juriya da bajinta irin ta MAZAN JIYA masu juriya a filin fama,

A wannan lokaci babu abin da kunne ke ji face ihun mazaje da ƙarar karafniyar ƙarafa gami da haniniyar dawakai, ƙura ta turnuƙe sararin samaniya aka fara yiwa ƙasa ado da jini, sassan jikkunan bil'adama suka fara shawagi a sararin samaniya suka zubowa ƙasa tamkar ana ruwan su ne daga saman,

Nan fa gari ya hautsi ne sakamakon guje-gujen al'umma gami da ifice-ificen su.

Bayan waziri Yazid ya yi umarni an afkawa birnin Zainul-Ansar da yaƙi sai kawai ya tuntse ldanuwanshi ya karanta ɗalasiman tsafi, Haƙiƙa masu iya magana sun yi gaskiya da suka ce "Tabbas "Makashin ka yana tare da kai" kuma tabbas ba a gane mutum a fuska, Inda a ce mutum yana tsaye a lokacin da waziri Yazid ke karanta ɗalasiman tsafin sai ya rantse ya ce bai Kasance musulmi ba,

Ko da gama rufe bakinshi sai ya shafi wani guru a damtsen shi na hagu na ɓace ɓat! tamkar bai taɓa wanzuwa ba.

Wannan shi ne abin da ya faru da su waziri Yazid da sarki Rakibu bayan sun kammala tara rundunar MAYAKA domin kai farmakin Bazato birnin Zainul-Ansar domin hamɓarar da sarki Nu'umanu daga kan karagar mulki.

Al'amarin shugaban dakarun sarki Lamsarul-Azlam kuwa wato Sadauki Hukaiza tun sa'adda aka fyaɗa shi da ƙasa sakamakon yunƙurin da ya yi na gudanar da bincike game da yaro Usaiba mai hatimin takobin Saiful-zayyad da jaruma Rusayyat ta ceci rayuwar shi sai ya yi yunƙurin miƙe wa tsaye amma sai ya ji ya kasa,

Ko da sauran dakarun suka fahimci cewa ya kasa miƙewa tsaye sai suka zaburi dawakansu suka yunƙura izuwa inda ya ke,

Ko da ukaiza ya fahimci aniyar su sai kawai ya dube su ya daka masu tsawa cikin matuƙar fushi ya ce da su "Ya ku waɗannan dakaru ku yi sani cewa a halin yanzu ba zai yiwu a ina tashi tsaye akwai buƙatar na ɗauki tsawon lokaci a wannan waje kafin jikina ya samu lafiya,

Abin da na ke so ku yi kawai shi ne ku koma izuwa ga mai girma Lamsarul-Azlam ku labarta masa abin da ya wakana gare mu, domin ko da ba ku koma gare shi yana ba za ku iya tsere mashi ba".

Ko da jin wannan batu daga bakin Ukaiza sai hankulan dakarun ya yi mummunan tashi Suka ce a cikin zukatansu tabbas a halin yanzu muna cikin tsaka mai wuya kuma gaban mu tsini ne baya siyaki.
Wani garjejen ƙato daga cikin mayakan ya buɗi baki cikin ƙarfin hali ya ce "Ya shugabana sanin kanka ne cewa matsawar mu ka je da wannan mummunan labari ga mai girma Lamsarul-Azlam to hukuncin kisa ya tabbata a gare mu",
Ukaiza ya ce "Ai ko da baku koma zuwa gare shi sanin kanku ne cewa zai iya tura wata Annobar da zata hallaka ku ku yi mutuwar wulakanci,
Saboda haka yanzu shawara dai ta rage ga mai shiga rijiya".
Sa'adda Ukaiza ya zo nan azancen shi sai jikin dakarun ya yi sanyi kawai sai suka sakarwa dawakansu linzami suka durfafi wani ɓangare a dajin suna masu tsala gudu zukatansu cike da matuƙar tsoro.

***

'yar gajeriyar tafiya Rusayyat ta yi a cikin gidan sarautar ta iso wata ƙasaitacciyar turaka da aka cika ta da nau'ikan kayan ƙawa da alatun jin daɗin rayuwar duniya, kai tsaye ta kunna kai izuwa ciki,
Zaune ta same shi ya tafka wani uban tagumi ta isa gare shi ta zauna daf da shi ta sanya hannayenta biyu ta dafa kafaɗunshi, Haka ne ya sanya ya dawo daga duniyar tunanin da ya yi fana'i a ciki,
Sannan ta dube shi fuskarta cike da annuri ta ce "Ya uban 'ya'yana shin ina dalilin wannan tagumi na ka ?.
Ko da jin wannan batu sai Fitinatul-Amir ya mayar mata da martanin murmushin da ƙara wa fuskar shi kwarjini ya yi gyaran murya ya ce "Ya abar bege na dare da rana ki yi sani cewa bakomai ne ya sanya ni a cikin wannan hali sai bisa rashin samun Magaji,
Babban abin da ke dugunzuma hankalina shi ne yadda har yau na gaza gano inda yaro mai hatimin takobin Saiful-zayyad yake wanda shi kaɗai ne ya matsala wajen burina namu.
Ko da jin wannan batu sai Rusayyat ta yi murmushi a karo na biyu har kyawawan haƙoranta suka bayyana farare ƙal!, Cikin zazzaƙar murya mai daɗi tamkar sarewa ta ce " Ya muradin raina ka kwantar da hankalinka tamkar tsimma a randa ka yi sani cewa a yau na samo wata gagarumar tsintuwa da zata maye gurbin rashin magaji a gare mu.
Cike da alama matuƙar mamaki Fitinatul-Amir ya dube ta ya ce " Ya farin cikin rayuwata shin wace irin tsintuwa ce kika yi da zata maye mana gurbin magaji?
Da jin wannan tambaya sai Rusayyat ta miƙe tsaye tsam! daga kan kujerar ta durfafi ƙofar fita daga turakar tana mai yafito Fitinatul-Amir da hannu tana nuna cewa ya biyo bayanta,
Ba tare da bata gardama ba ya miƙe tsaye ya yi ko yi da ita,
Lokacin da suka fice daga turakar sai suka wanzu suna tsara saƙo da lungu a gidan sarautar, duk inda suka gifta sai ka ga dakaru, barori, dakaru haɗe da bayi na zubewa ƙasa suna kwasar gaisuwa cikin girmamawa.
Wannan shi ne abin da ya faru tsakanin Jaruma Rusayyat da mai gidanta Sadauki Fitinatul-Amir.

***

Dukkan abin da ya wakana tsakanin Jaruma da Rusayyat da shugaban dakaru sadauki Hukaiza,
Sarki Lamsarul-Azlam ya gani a cikin madubin tsafin shi a lokacin da yake zaune a cikin ƙasaitacciyar turakar shi ta shaƙatawa,
Ko da ganin wannan al'amari sai ya cika da matuƙar baƙin ciki maral-musaltuwa ya buɗi baki cikin kakkausar murya yana mai cewa "Haƙiƙa jaruma Rusayyat ta aikata laifi mafi muni a gare ni da ba zan taɓa yafe mata ba face ta miƙo mani yaro mai hatimin takobi,
Ko da yazo nan azancen shi sai ya sake baje alƙalumman sihirin ya sake nutsawa cikin halarar tsafin domin ya ga irin wainar da duniya ke toyawa,
Abin da ya gani abinciken shi ne ba shi da wani aiki da ya huce ya ga ya gano sabuwar hanyar mallakar yaro mai hatimin takobi.

***

Lokacin da aljani Lattul-kifas ya tsala da matsanancin gudu a sararin samaniya sai ya wanzu yana ratsa giza-gizai,
Tafiyar dakiƙa hamsin kacal ya yi ya iso wani ƙasaitaccen gida mai girma da tsawo tamkar gari guda,
Ko da ya yi arba da gidan sai kawai ya saki fuka-fukanshi ya yi ƙasa luuh! ya sauka a turba nesa ƙaɗan da inda gidan ya ke, Nan take ya kama kalle-kalle da dube-dube tamkar ɗan ƙauye ya shigo birni,
Wani abu da ya ba shi mamaki game da gidan shi ne yadda aka yi ginin shi da zallar waɗansu irin duwatsu masu ƙyalli tamkar gilashi, an yiwa dukkan katangun gidan ado da wani irin hatimin sarauta gami da turanni mabanbantan launuka masu kyawun gani da ƙamshi,
Duk inda mutum zai taka a harabar gidan an yi daɓe da koren yaƙutu,
Wohoho! haƙiƙa babu wani attajiri ko BASARAKE da zai yi arba da wannan gida face ya tabbatar wa da kanshi cewa GABA DA GABANTA, kuma sawun Giwa ya take na raƙumi,
Iya tsawon rayuwar aljani Lattul-kifas bai taɓa gani ko jin labarin gida mai ƙawatuwa tamkar shi ba,
Na rantse da gemun kakana boka Zamzarul-Dayyan ko wane ne mai mallakin wannan gida yakasance mutum mai girman matsayi a tsakanin duniyar mutane da aljanu domin wannan gida na shi a iya kiran shi da suna aljannar duniya",
Lattul-kifas ne ya yi wannan furuci a cikin ran shi ba tare da ya bayyana ba.
Ko da kammala furuci sai ya yunƙura ya durfafi gidan domin ya ganewa kwarkwatar idanunshi, domin masu iya magana na cewa gani ya kori ji, Ai kuwa sai ya hango waɗansu irin gabza-gabzan dakaru na jinsin MUTUM DA ALJAN ɗauke da miyagun makamai bila-adadin masu matuƙar barazana ga duk wata halitta mai numfashi,
Sa'adda ya yi arba da su sai firgita ainun tsoro ya kama shi duk da kasancewar gwarzon mayaƙi mai dakakkiyar zuciya,
Amma abin da ya ba shi mamaki shi ne dakarun ko ɗaga kai ba su yi ballantana su yi yunƙurin afka mashi,
Shin ko dakarun ba sa iya gani na ne ?,
Amsar tambayar da ya kasa bawa kanshi kenan kawai sai ya takaici Idanuwansu ya falfala da gudu domin ya shiga zuwa gidan batare da sun gan shi ba.

Kaico! haƙiƙa masu iya magana sun yi gaskiya da suka ce "kifi na ganin ka mai jar koma" ya yin da ya rage saura taku uku ya ketare katangar gidan sai dakarun suka yi ɗauki kan shi suka yi masa ƙawanya saboda girman dakarun da yawan su sai aljani Lattul-kifas ya zamo tamkar an ajiye kwanya guda ɗaya a gaban dubban karnuka,
Tamkar haɗin baki a lokaci guda dakarun suka afka masa da dukkan ƙarfin su suna ihu da kururuwa mai firgita ZARATAN JARUMAI komai matuƙar yawan su,
Kaico! haƙiƙa komai dakewar zuciyar jarumi da rashin tsoron shi idan ya ga yadda dakarun ke kururuwar suna ɗaga makamansu izuwa sama dole ne ya ɗimauce,
Ko da ganin hakan sai Lattul-kifas ya yi wuf! ya zare wata sharbebiyar takobi a damtsen shi ya tare su aka kacame da masifaffan artabu mai matuƙar muni daban tsoro, ƙarar karafniyar ƙarafa gami ihu da kururuwar mazaje ta cika dodon kunne.
Wannan shi ne abin da ya faru da aljani Lattul-kifas da boka kaddad ya tura domin ya ɗauko mashi yaro mai hatimin takobin Saiful-zayyad.

***

Al'amarin waziri Yazid kuwa tun sa'adda ya ɓace cikin alƙalumman sihiri bayan ya yi umarni an farmaki birnin Zainul-Ansar da yaƙi bai bayyana a ko ina ba sai a tsakiyar gidan sarauta,
Ko da bayyanar shi sai ya zare wata sharbebiyar takobi a gadon bayanshi ya afkawa dakarun gidan da sara da suka yana kutsawa cikin gidan sarautar.
Sa'adda Sarki Nu'umanu ya ji gidan sarautar ya kaure da guje-guje gami ifice-ificen jama'a sai kawai ya ruga zuwa turakarshi, jim kaɗan sai ga shi ya fito shirye cikin matsananciyar shigar yaƙi mai matuƙar kwarjini da ban tsoro, fararen sulken ya saka haɗe da koren rawani, ya rataya waɗansu zaratan takubba biyu a gadon bayanshi,
Kawai sai ya durfafi turakar uwar gidan shi lawisat, Ya na isa dakarun suka wangame kofa ya kunna kai ciki,
Sa'adda lawisat ta yi arba da maigidan ta a cikin wannan hali sai kawai ta faɗa kan ƙirjin shi ta rungume shi ta fashe da kuka mai tsuma zuciya,
Da ga can sai sarki ya janye jikinshi daga na ta suka fuskanci juna,
"Shin ina dalilin wannan hawaye na ki ya Sarauniyar zuciyata?,
Ko da jin wannan tambaya sai lawisat ta buɗi baki cikin alamun damuwa ta ce "Ya uban 'ya'yana ka yi sani cewa na ji a jikina cewa wannan yaƙi da zaka fita ba alkairi ba ne, ma'ana shi ne zai zamo ajalinka.
Ko da jin wannan batu sai sarki Nu'umanu ya sanya hannayenshi ya share mata hawayen dake kan fuskarta ya dube ta cikin alamun tsantsar tsantsar so da ƙauna ya ce "Ya Annurin kalbina ki yi sani cewa RAYUWA DA HALAKA duk a hannun Allah (SWT) suke komai zai kasance wajibi ne a gare ni na fita na kare rayukan al'ummata,
Kada ki manta cewa muna kan bisa TAFARKIN TSIRA abokan gabar mu kuwa suna bisa TURBAR AJALI, Domin haka da yardar Ubangijin halitta za mu samu nasara a wannan yaƙi kuma na dawo gare ki cikin ƙoshin lafiya,
Fatana shi ne ki Kasance mai yi mani fatan alheri da nasara, idan kuma ta Allah ta kasance ki roƙa mani gafara a wajen Ubangiji".
Lokacin da Sarki yazo nan azancen shi sai lawisat ta sake fashewa da kuka a karo na biyu, Dakyar da siɗin goshi ya samu ya lallashe ta ya fice turakar suna masu zubar da hawayen rabuwa da juna.

Yana fitowa ya falfala da azababban gudu zuwa cikin gidan sarautar ba tare da ya haye bisa doki ba.

Wannan shi ne abin da ya faru a birnin Zainul-Ansar bayan waziri Yazid ya kai farmakin Bazato zuwa birnin.

***

A can ƙasar Darul-Ashmar kuwa sarki Lamsarul-Azlam ya shafe tsawon kwanaki biyu yana gudanar da bincike domin ya gano hanyar da zai hallaka yaro mai hatimin takobin Saiful-zayyad,
Abin da ya gano shi ne ɗin shi ne ba zai iya hallaka yaro mai hatimin ba face a ranar da sadauki Fitinatul-Amir ya gano cewa yaro Usaiba shi ne wanda yake farauta tsawon shekaru,
Sa'adda ya ga wannan al'amari sai ya cika da matuƙar farin ciki maral-musaltuwa,
Shin mene ne dalilin da ya sanya sarki Lamsarul-Azlam ke farautar yaro usaiba mai hatimin takobi dalilin hakan kuwa shi ne.

Sarki Lamsarul-Azlam ibn Rauzil ya kasance GWARZON BASARAKE kuma gawutaccen mayaƙi da ya yi shura a ilimin tsafi, daɗin daɗawa kuma ya kasance azzalumi na gaban kwatance,
Gaba ɗaya jama'ar birnin Darul-Ashmar babu wnada yake jin daɗin mulkin shi face fadawa shi kaɗai,
Saboda matuƙar zaluncin shi ne ya sanya ya mamaye birane da ƙasashen da ke makwabtaka da shi sun yi MUBAYA'A a gare shi ta ƙarfin tsiya, Bisa wannan dalili ne ya sanya ya zamo babu mashahurin sarki tamkar shi a kaf nahiyar.

Wata rana da sulu-sainin dare sarki Lamsarul-Azlam na zaune a cikin turakarshi ya baje alƙalumman sihirin yana gudanar da bincike domin ganin halin da duniya ke ciki,
Yana cikin wannan hali ne sai kawai ya taƙarƙare ya kurma wawan ihu da ya mamaye gidan sarautar ya amsa kuwwa izuwa ko ina, Al'amarin da ya yi matuƙar janyo hankalin dakarun gidan kenan suka zare makaman su suka rugo izuwa turakar,
Ba wani abu ne ya sanya shi wannan ihu ba face wani al'amari da ya gani a madubin tsafin shi,
Abin da ya gani ɗin shi ne wani yaro mai shekaru tara dake ɗauke da zanen hatimin takobin Saiful-zayyad a gadon bayanshi da zai zamowa sarakunan duniya ƙadangaren bakin tulu kuma ciwon idanu, zai kawo ƙarshen mulkin duk wani azzalumi a doron ƙasa kuma zai samu ɗaukaka fiye da kowa ne sarki a duniya,
Yaron yakasance ɗa ne ga wani wani sarki da ake kira da suna Hidyal na birnin Baitul-Hazwar dake yamma maso gabashin duniya a gaban tekun baharul-sawara,

## BABI NA TAKWAS

Lokacin da dakarun suka iso turakar sai suka yi turus! ba wani abu suka gani ba face dakarun dake gudanar da tsaro alamun dake bayyana cewa babu wani al'amari da ya gudana mara kyawu,
A lokaci guda sarki Lamsarul-Azlam ya tsuke bakinshi daga sannan ya ƙwalla wani hadimin shi kira mai suna Hukaiza ya bayyana a gare shi, sarki ya dube shi ya ce "Ya kai Hukaiza ina so ka

jagoranci MAYAKA izuwa birnin Baitul-Hazwar dake iyaka da gabar tekun baharul-sawara ku hallaka duk wata halitta dake ciki koda kiyashi kada ku bari a raye,
Cikin matuƙar ladabi Hukaiza ya miƙe ya fice daga turakar ba tare ya ce uffan ba.
Wannan shi ne dalilin da ya sanya sarki Lamsarul-Azlam ke farautar yaro usaiba mai hatimin takobin Saiful-zayyad.
Sarki Lamsarul-Azlam na zaune a bisa KARAGAR MULKI cikin suturu na alfarma irin na hamshaƙan sarakai yana sanye da kambun Sarauta a kanshi a hannunshi yana riƙe da kwagiri na sarauta,
Lamsarul-Azlam yakasance dattijo mai kamanin shekaru hamsin, fatar jikinshi wankan tarwaɗa ce, yana da ƙasumba da gemu mai tsawon kamu biyu baƙaƙe siɗik da suka ƙara bayyana kyawun fuskarshi, Yana da rubɗeɗen ciki tamkar an kifa kwarya, kallo ɗaya za ka yi mashi ka fahimci cewa ya cika GWARZON BASARAKE mai tarwatsa mazaje a filin fama.
A gefen hannun shi na dama kuwa 'yar shi gimbiya Sharilat zaune bisa kujera ta alfarma sanye cikin ƙayatattun tufafi na alfarma da suka bayyana tsantsar kyawun surar ta,
Gimbiya sharizat ta kasance mai matsakaicin kaurin jiki, idanuwanta dara-dara ne farare ƙal! masu tamkar tacecciyar madarar shanu, hancinta dogo mai lankwasa, a ƙasan shi an tsaga wani madaidaicin baki da laɓɓan shi suka jajur, wuyanta mai kyawu ne tamkar na barewa, kirjinta a cike yake yaƙe kuma a tsaye kyam bai rankwafa ba, cikinta a shafe yake tamkar bata taɓa cin komai ba, ƙuguntа a tsuke yake daga baya kuma ya yi tudu tamkar a ɗora tuffa ta zauna a kai, tana da zara-zaran gaɓoɓi da fatar su ta kasance mai sheƙi, gashin kanta baki siɗik mai ƙyalli tamkar gilashi ya zuba akan gadon bayanta,
Wohoho haƙiƙa duk inda kyawu yake gimbiya Sharizat ya cika, babu wani ɗa namiji da zai yi arba da ita face ya kamu da matuƙar soyayyar ta,
A rayuwar Sharizat bata da wani buri da huce taga yaro mai hatimin takobin Saiful-zayyad domin ya tseratar da shi daga sharrin mahaifinta sarki Lamsarul-Azlam, domin ta ga ta kawo ƘARSHEN ZALUNCI da yake yiwa al'umma,
Bisa wannan dalili ne ya sanya duk sa'adda sarki zai gudanar da bincike game da yaro mai hatimin takobin sai ita ma ta shiga binciken bisa halarar tsafin ta domin gano ko yaro mai hatimin ya bayyana.
A wannan lokaci duk inda mutum ya kalla a fadar babu abin da zai gani face kawunan bil'adama rututu babu masaka tsinke tamkar DANDAZON MAYAKA,
A gefe guda kuwa 'yan majalissar sarki na zaune a bisa shimfiɗu na alfarma kawunan su a sunkuye tamkar masu neman gafara.
Ana cikin wannan hali ne sarki Lamsarul-Azlam ya lura cewa lokacin ta shi daga fada ya yi domin haka sai ya miƙe tsaye tsam! daga kan karagar shi ya yaƙi matattakalar fadar ya sauko ƙasa ya rike hannun gimbiya Sharizat suka nufi wata ƙofa ta musamman a fadar take waɗansu ZARATAN DAKARU ma'abota baƙaƙen tufafi suka mara masu baya har suka ƙule izuwa cikin ƙofar,
Nan take fadar ta watse kowa ya kama gaban shi.

***

Tafiyar daƙiƙa hamsin Rusayyat da mai gidanta Sadauki Fitinatul-Amir kacal suka yi suka iso zuwa turakar da su yaro usaiba ke ciki, cikin hanzari dakarun masu tsaro suka wangame ƙofar

shiga tare da miƙa gaisuwa, kai tsaye Rusayyat ta jagoranci mai gidanta har zuwa gadon da su Usaiba ke kwance suka zauna a gefen shi,
Sa'adda Fitinatul-Amir ya yi arba da yaro Usaiba sai zuciyarshi ta buga da ƙarfi alamun tsoro ƙarara suka bayyana a fuskarshi, sannan ya mayar da duban shi ga Hairat ya ɗauki tsawon lokaci yana nazarin kyakkyawar fuskarta,
Daga bisani ya mayar da duban shi ga Rusayyat cikin tattausan murmushi da ya fi kama da yaƙe ya ce "Madalla da wannan tsuntuwa ya abar ƙaunata haƙiƙa na kasance cikin matuƙar farin ciki maral-musaltuwa, kuma naji a jikina cewa waɗannan yara za su maye mana gurbin magaji a gare mu,
Yanzu zan tafi zuwa ya sake komawa barci domin na wartsake kafin lokacin fita fada ya yi zan samu lokaci sai mu ƙara tattaunawa akan wannan al'amari".
Gama faɗin hakan ke da wuya sai ya miƙe tsaye tsam! ya taka da ƙafafuwanshi ya nufi ƙofar fita daga turakar yana mai waigen uwar gidan shi suna yiwa juna lallausan murmushi mai gusar da dukkan damuwa.
Koda ficewar shi sai Rusayyat ta faɗa izuwa kogin tunani, Abu na farko da ya faɗo mata a rai shi ne,
Anya kuwa mai gidan ki ba bincike ya tafi ya gudanar akan waɗannan yara ba ki lura da irin kallon da ya yi masu mana alamu suna nuna bai aminta da su ba,
Wani tunanin da ya faɗo mata shi ne mai zai hana ko gudanar da binciken domin ki gano gaskiya al'amari game da waɗannan yara,
Sa'adda Rusayyat tazo nan a tunanin ta sai sai baje alƙalumman sihirin ta ta shiga gudanar da binciken.
Wannan shi ne abin da ya faru tsakanin shugaban'yan fashin duniya Sadauki Fitinatul-Amir da uwar gidan shi jaruma Rusayyat.

***

Sa'adda sarki Nu'umanu ya falfala da azababban gudu hannunshi riƙe da takobin tsirara yana mai fuskantar hanyar da zata sada shi da kofar fita daga gidan sarauta,
Yana cikin wannan hali ne ya hango wani badakare fuskarshi rufe da rawani ldanuwanshi kaɗai ake gani ya durfafo inda yake ya na hallaka dakarun dake gaban shi yana samarwa da kanshi hanya ya ƙarfin tsiya.
Sa'adda sarki Nu'umanu ya lura da irin muguwar ɓarnar da badakaren ke yi mashi sai kawai ya ƙwalla kabbara da ƙarfi ya durfafi inda yake cikin mugun tanadi.
Lokacin da ya rage bai huce taku shida a tsakanin su ba sai badakaren ya dako wawan tsalle tamkar an harbo shi daga cikin baka ya dira a daf da inda sarki Nu'umanu yake suka tari juna aka ruguntsume da azababban yaƙi mai matuƙar kwarjini da ban sha'awa,
Suka wanzu suna kaiwa juna sara da suka cikin matuƙar zafin nama JURIYA DA BAJINTA ta gaban kwatance, Duk sa'adda makaman yaƙin su suka haɗu da juna sai dai kaga tartsatsin wuta ya tashi gami da ƙara mara daɗin saurare.
Kaico! Haƙiƙa yaƙi abin tsoro ne da tashin hankali wanda bai san shi ba shi ne yake fatan zuwan shi, domin yaƙi shi ne ke ƙarya tattalin arziki da duk wani jin daɗin rayuwa ta ɗan adam, Inda a ce mutum zai ha yadda ruhikan mutane ke rabuwa da gangar jikin su yara da mata na zamowa marayu dole ya zubar da hawayen baƙin ciki, Duk da kasancewar dare ya tsala amma

sai garin ya zamo tamkar safiya ce saboda yadda haɗuwar makaman yaƙi ke haddasa wani haske a sararin samaniya.

Aɓangaren sarki Rakibu da sarkin yaƙi lauzar kuwa sun wanzu suna yiwa dakarun birnin Zainul-Ansar muguwar ɓarna yazamana cewa duk inda suka sanya a gaba sai dai kaga dakaru na zubewa ƙasa matattu tamkar ana sassabe a gonar auduga,

A ɓangaren dakarun birnin Zainul-Ansar kuwa waɗansu zakwakuran MAYAƘA ne masu zafin nama gami da nacin tsiya keta faman yiwa dakarun haɗin gwiwa muguwar ɓarna ,
Nan fa jini ya dinga kwaranya tamkar na ɓalle ƙorama, sassan jikkunan bil'adama suka dinga shawagi a sararin samaniya suna zubowa ƙasa tamkar ana ruwan su ne daga saman,
Hankakan mutuwa ya wanzu yana kai komo wajen ɗaukar rayuka, gidaje suka dinga kamawa da wuta suna rushewa, Musulmi na yin kabbara kafirai na ihu da kururuwar banza, ƙarar karafniyar ƙarafa gami da ihun mazaje suka cika dodon kunne, dawakai suka dinga jefar da mahayansu suna nausawa izuwa cikin daji saboda azabar yaƙi,
Komai kallon ƙurillan mutum ba zai iya bambance ɓangaren da suke da nasara ba saboda yadda filin yaƙin ya yamutse,
Lokacin da sarki Rakibu da sarkin yaƙi lauzar suka ga irin mummunar ɓarnar da waɗannan zakwakuran MAYAƘA na dakarun Musulunci ke yi masu sai suka canza salon faɗansu,
Yazamana cewa sun ƙara zage damtse wajen ragargazar dakarun sarki Nu'umanu babu sassauci,
Ba wasu ba ne waɗannan mayaƙa da ke ɓangaren dakarun Musulunci ba face shugaban baitul-mali, galadima tare da sarkin fada uwaisu,
Koda shugaban baitul-mali ya lura da irin ɓarnar da su sarki Rakibu ke yi masu sai ya canza salon faɗan shi, Da ganin hakan sai sarkin fada da galadima suka yi koyi da shi yazamana sun zare sabbin makaman a jikin su sun ƙara afkawa abokan gaba.

A ɓangaren sarki Nu'umanu da badakare kuwa sun shafe tsawon Sa'a ɗaya suna kaiwa juna sara da suka cikin matuƙar zafin nama juriya da bajinta domin salwantar da rayukan juna amma babu alamun nasara ga kowa ne ɓangare,
Al'amarin da ya yi matuƙar ɗaurewa Sarki Nu'umanu kai kenan kuma ya ba shi mamaki domin tun da yake artabu da manyan jarumai hakan bai taɓa wanzuwa ba, ya yin da ya zo nan a tunanin shi sai ya cigaba da ambaton tsarkakan sunayen Allah a cikin ran shi yana neman taimakon shi,
A ɓangaren badakaren kuwa ba haka abin yake ba domin ba shi da wani buri da ya huce ya ga hallaka sarki Nu'umanu,
A cikin gidan sarauta kuwa al'amarin gimbiya lawisat uwar gidan sarki Nu'umanu kuwa duk sa'adda ta ji gidan sarautar ya kaure da guje-guje gami ifice-ificen jama'a sai hawayen su sake kwaranya daga idanuwanta tana tunanin halin da mai gidanta sarki Nu'umanu ya ke ciki,
Wannan shi ne abin da ya wakana a can birnin Zainul-Ansar.

***

Lokacin da aka ruguntsume da azababban yaƙi mai matuƙar kwarjini da ban sha'awa tsakanin aljani Lattul-kifas da waɗannan dakaru masu tsaron wannan ƙayataccen gida, Sai yaƙin ya zamo abin tsoro da fargaba yazamana cewa dakarun suna kaiwa aljani Lattul-kifas sara da suka cikin matuƙar zafin nama JURIYA DA BAJINTA suka yanyame shi tamkar yadda ƙudaje ke yanyame ƙwallon ma Gwari,

Aljani Lattul-kifas ya wanzu yana kare hare-haren dakarun cikin juriya da nacin tsiya duk sa'adda da ya kare harin mayaƙan sai kaga ya durƙushe ƙasa saboda ƙarfin saran dakarun idan kuwa shi ya kai masu hari sai dai takobin shi ta nutse a cikin ƙarƙashin ba tare da ya samu nasarar koda lakutar jikin ɗayan su ba,
Sai da aka shafe tsawon sa'a ɗaya ana wannan ƙazamin artabu babu sassauci babu nasara ga kowa ne ɓangare,
Al'amarin da ya yi matuƙar ɗaurewa Lattul-kifas kai kenan kuma ya zurfafa zuwa ƙogin tunani,
Abu na farko da ya faɗo mashi a rai shi ne kasancewar shi GWARZON BASARAKE mai tarwatsa maza a filin fama komai matuƙar yawan abokan gaba yana iya maishe su fawa cikin 'yan daƙiƙu, amma sai gashi waɗannan dakaru sun gagare shi hallakawa,
Sannan shin Waɗannan dakaru bana sihiri na ne kuwa? Idan haka ne shin tsakanin mai mallakin wannan gida da mai gidana boka kaddad wane ne yafi wani shahara?
Wani ɓangaren a zuciyarshi na cewa da shi ai shi ilimin tsafi Kogi ne komai nutson ka ba zai yiwu ka ƙure ƙarshen shi ba.

Lokacin da aljani Lattul-kifas yazo nan a tunanin shi sai hankalin shi ya dugunzuma ainun abin da ya ɗugunzuma hankalin na shi shi ne haƙiƙa a kowa ne lokaci ƙarfin damtsen shi zai ragu ainun kuma hakan zai iya bawa dakarun nasara akan shi, domin haka sai ya fusata ainun ya sake zage zage damtse yana cigaba da kai masu hari ta ko ina tamkar wani ifritu,
Yana cikin yaƙin ne kawai sai ya yi jifa da takobinshi ya shiga yaƙar dakarun da tsagwaron ƙarfin damtsen shi.

Wohoho! haƙiƙa "idan kiɗa ya canza dole ne rawa ta canza" kuma masu iya magana na cewa idan kaji ana ga ƙi gudu to sa gudu ne bai zo ba" faruwar hakan ke da wuya sai aljani Lattul-kifas ya gano lagon dakarun yazamana cewa duk wanda ya gabzawa naushi a wuya sai kaga ya karye jikake ruƙus ƙas! a wasu sai dai ka ga ya kama badakare ya yagashi gida biyu yana tamola da dasu,
Nan fa sassan jikkunan dakarun suka dinga shawagi a sararin samaniya suna zubowa ƙasa, jini ya dinga kwaranya tamkar an ɓalle ƙorama, ƙura ta turnuƙe sararin samaniya, ihu da kururuwar mazaje haɗi da ƙarar karafniyar ƙarafa ta cika dodon kunne,
Kaico! haƙiƙa a wannan rana waɗannan dakaru suna ganin tashin hankali gami da annobar mutuwa,
Kafin shuɗewar daƙiƙa ɗari biyu Lattul-kifas ya ragargazi dakarun baki ɗaya, Babu wani a cikin su da rage a ruhi a tare da shi.

Wani abu da ya bawa Lattul-kifas mamaki kuma ya ɗaure mashi kai shi ne yadda aka yi takobinshi a ɗazu taƙi yin tasiri akan dakarun, Bayan cewa komai ya sara da takobin koda ƙarfe take ya ke narkewa, Abin da bai sani ba shi ne sihirin dake jikin takobin ta shi ce ba zai yi tasiri a jikin dakarun ba,
Koda samun wannan gagarumar nasara sai kawai ya taƙarƙare ya bushe da dariyar mugunta gami da sanya hannayenshi biyu yana dukan ƙirjinshi tare da yiwa kanshi kirari yana mai cewa.

"Sai ni GOBARAR DAJI maganin ƙananan hatsabibai.
"KAIFIN TAKOBI nake mai raba tsakanin masoya.
"KOGON ANNOBA nake MUTUWAR SADAUKAI.
"Sai ni kangarau uban gagarau mai shayar da duniya GUGUWAR HALAKA.

"Na ci dubu sai ceto karo da ni dai-dai yake da buɗe taskar ANNOBA DARI.
Haka ya wanzu yana yiwa kan shi wannan kirari, bayan ya kammala ne ya ya lura cewa duhun dare ya fara bayyana a sararin samaniya domin haka sai ya yanke shawarar ya kwana a nan da safe sai ya shiga wannan gida, ko da kammala wannan shawara sai kawai ya shimfiɗe fuka-fukanshi ya bararraje ya fara sharar barci.
Wannan shi ne abin da ya faru da Sarkin matasan aljanu na baƙaƙen fata aljani Lattul-kifas, a kan hanyar shi ta farautar yaro usaiba mai hatimin takobin Saiful-zayyad.

**

Yalwataccen daji ne mai cike da tarin ni'ima, duwatsu, ƙoramu, da tarin dogayen bishiyu, wata irin ni'imtacciyar iska mai tattare da ni'ima ya kaɗai sassan tsirrai suna rangaji, waɗansu irin kyawawan tsuntsaye na shawagi a sararin samaniya suna fitar da wani irin sautin kuka mai daɗin saurare,
Komai ƙasaitar BASARAKE ko attajiri idan ya tsinci kanshi a wannan waje dole ne yakasance cikin nishaɗi da annashiwa,
Amma abin mamaki sai ga shi wata halitta ta wanzu a wannan waje amma ta kasance cikin matuƙar baƙin ciki, bakomai ne zai tabbatar maka da hakan ba sai idan kayi arba da wani mutum bisa ƙarƙashin wata itaciya ya tafka uban tagumi hawaye na zuba daga idanuwanshi, ba wani ba ne wannan Mutum ba face Sadaukai Hukaiza shugaban rundunar sarki Lamsarul-Azla, Ba wani abu ba ne ya sanya shi zubar da hawayen ba sai bisa tunanin irin baƙin zaluncin da sarki Lamsarul-Azlam yake yiwa al'umma, ya sanya shi kashe rayukan al'umma da ba su ji ba su gani ba,
Wani tunanin da ya faɗo masa shi ne shin yaushe ne zai cire zuri'ar su daga KANGIN BAUTA waɗanda suke a matsayin bayi a masarautar shi, ya zama wajibi a gare ka da ka kwashe iyalan ka domin ku tafi can wata nahiyar daban domin yin Sabuwar rayuwa,
Wata zuciyar kuma na cewa da shi kada ka manta da wasiyyar da mahaifinka ya yi maka inda yake cewa " ya ɗana kada ka taɓa cewa zaka yi gaggawa wajen ɗaukar fansa akan sarki Lamsarul-Azlam domin kuwa gaggawa aiki ne na da nasa ni ka riƙe haƙuri haƙiƙa nasara tana tafe a gare ka da zaka cika mani burina na cire zuri'ar mu daga BAUTAR MUTUWA a ƙarƙashin ikon sarki Lamsarul-Azla.
Ya yin da Hukaiza yazo nan a tunanin shi sai hawaye suka ci gaba da kwaranya daga idanuwanshi,
Wannan shi ne abin da ya faru ga Sadauki Ukaiza shugaban dakarun sarki Lamsarul-Azlam da ya tura domin farautar yaro usaiba mai hatimin takobin Saiful-zayyad.

Mu haɗu a TAFARKIN TSIRA 5 domin jin cigaban wannan ƙayataccen labari.
Daga mai ɗebe maku kewa a kullum da koyaushe.

MANSUR USMAN SUFI
Sarkin Marubutan Yaki
08137237071

TAFARKIN TSIRA 5
Rubuta Labari
MANSUR USMAN SUFI
Sarkin Marubutan Yaki
Wthapp Number
08137237071

BABI NA TARA

Kamar yadda Jaruma Rusayyat ta faɗa haka al'amarin yakasance, domin kuwa mai gidan ta Fitinatul-Amir yana shiga izuwa cikin turakarshi sai ya ɓaje dukkan alƙalumman sihirin shi ya shiga gudanar da bincike bisa halarar tsafin shi akan yaro usaiba sai da ya shafe tsawon sa'o'i yana gudanar da bincike batare da ya samu nasarar gano komai ba,
Al'amarin da ya yi matuƙar dugunzuma hankalin shi kenan kuma ya fusata shi ainun, Babban abin da ya fi dugunzuma hankalin shi shi ne lokacin da ya haɗa idanu da yaro Usaiba sai ya ji zuciyar shi ta buga da ƙarfi ya kasa samun nutsuwa, anya kuwa ba shi ne yaron da nake farauta ba,
Nan fa ya sake zurfafa cikin Kogin tunani domin samun mafita, Tsawon daƙiƙa goma yana wannan nazari sai daga bisani ne ya samu mafita, Mafitar kuwa ita ce kawai ya duba gadon bayan Usaiba domin ya tabbatar da zargin shi,
Ko da samun kyakkyawar mafitar sai ya cika da matuƙar farin ciki maral-musaltuwa, kawai sai ya kishingiɗa domin ya huce gajiyar da ke tare da shi.
A ɓangaren Rusayyat kuwa lokacin da ta gudanar da binciken ta bisa halarar tsafin ta nan take ta gano cewa yaro Usaiba shi ne yaro mai hatimin takobin Saiful-zayyad da mai gidanta Sadauki Fitinatul-Amir ya ke farauta,
Sa'adda ta ga wannan al'amari sai hankalin ta ya dugunzuma ainun, Cikin hanzari ta sanya hannayen ta ta kware rigar dake jikin Usaiba tana duba gadon bayanshi nan take ta yi arba da hatimin takobin Saiful-zayyad,
Ko da ganin hakan sai hankalin ta ya dugunzuma ainun fiye da kowa ne lokaci bakomai ne ya dugunzuma hankalin ta ba sai domin ta tabbatar da cewa matuƙar mai gidanta Fitinatul-Amir ya gano cewa yaro Usaiba shi ne yaro mai hatimin takobin Saiful-zayyad tabbas sai ya yi yunƙurin hallaka shi kuma bata da ikon hana shi,
Nan take ta shiga tunani mai zurfi domin samun mafita, Bayan shuɗewar daƙiƙa ashirin ta samu mafitar, Sai dai mafitar na da matuƙar wahalar gaske abin da za ta yi shi ne dole ta ɗauko wani garin magani dake ajiye a turakar mai gidanta,
Garin magani na farko zata yi amfani da garin maganin wajen shafawa Usaiba a gadon bayanshi domin ɓatar da zanen hatimin takobin,
Garin magani na biyu kuwa shi ne zai bayyana zanen hatimin idan aka shafa shi,

Nan fa hankalin ta ya sake ɗugunzuma ta sake zurfafa cikin Kogin tunani domin samun hanyar da zata shiga turakar mai gidannata har ta ɗauko garin maganin cikin sirri ba tare da asirin ta ya tonu ba,
Wannan shi ne abin da ya faru tsakanin shugaban'yan fashin duniya Sadauki Fitinatul-Amir tare da uwargidanshi jaruma Rusayyat.

BABI NA GOMA

Dakaru ne shirye cikin gagarumar shigar yaƙi su kimanin ɗari biyu riƙe da miyagun makamai suna tafe cikin hanzari, kallo ɗaya zaka yi masu ka fahimci cewa sun kasance azzalumai n gaban kwatance, Abin da zai tabbatar maka da hakan shi ne idan ka yi duba da fuskokin su sai ka yi tsakanin basu taɓa dariya ba.

Kai tsaye kasuwar birnin suka durfafa wacce ta cika maƙil da jama'a, duk inda mai kallo ya kai duban shi babu abin da zai gani face masu siye da siyarwa na yi, Duk wajen da dakarun suka durfafa a cikin kasuwar sai dai ka ga jama'a na dare suna buɗe masu hanya tare da tattare kotsan su tamkar sun hango mutuwar su,
Haka dai dakarun suka ci gaba da kutsawa saƙo da lungu na kasuwar suna muzurai tamkar za su ci babu, Sai da suka shafe tsawon daƙiƙa hamsin suna tafiyar sannan suka iso wani ƙasaitaccen gida mai girma da faɗin gaske da aka yi ginin shi da zallar duwatsun wuta masu ƙwarin gaske, Ba tare da wani jinkiri ba wani garjejen ƙato daga cikin mayaƙan ya matsa daf da ƙofar ya ƙwanƙwasa har sau uku da ƙarfi.

Jim kaɗan da faruwar hakan sai ƙofar ta buɗe kwatsam! sai ga wani dattijo ma'abocin cikar kamala ya fito daga cikin gidan hannunshi riƙe da wata jakar fata, Sannu a hankali har iso izuwa inda dakarun suke ya zube ƙasa ya kwashi gaisuwa ga wani Sadaukai daga cikin dakarun wanda da alama shi ne shugaban su,
Cikin matuƙar fushi shugaban dakarun ya saka mashi tsawa da ta sanya hantar cikin shi ta kaɗa ya dube shi ya ce "Ya kai Isham shin ina harajin mai girma Lamsarul-Azlam da ka saba bayarwa?,
Cikin dattijon na tsuma ya ajiye jakar dinaren da ke hannun shi muryar shi na sarƙewa ya ce "Ka.. ga..far ce ni ya shuga.. bana bisa jinkirin fi..to..wa na tare ku har ku..ka iso nan".

Shugaban dakarun mai suna Shahral ya bushe da dariyar mugunta sannan daga bisani ya murtuke fuska cikin kakkausar murya ya dubi wani Barde dake tsaye a hannun shi na dama ya ce "Ya kai Ruhaizu yi hanzari ka lissafa mani dinaren da ke cikin wannan jaka.

Kafin shugaba Shahral ya gama rufe bakin shi Barde Ruhaizu ya tsugunna ƙasa ya shiga lissafa dinaren, jim kaɗan ya dubi shugaba Shahral cikin ladabi ya ce "Dinaren ya cika yadda ake bukata ya shugabana".

Ko da jin wannan batu sai Shahral ya gyaɗa kai alamar gamsuwa sannan ya dubi dattijon ya ce "Sai ka kasance cikin shiri domin a koda yaushe zamu iya dawo wa domin sake ƙarbar wannan haraji.

Yana gama ya juya ya shige gaba sauran dakarun suka mara ma shi baya suka sake nausa wa cikin kasuwar suna tafiya cikin hanzari,
Suna cikin wannan tafiya ne kwatsam! bazato babu tsammani sai suka hango wata tsaleliyar kyakkyawar Budurwa tana sanye cikin fararen tufafi masu yalwa a gadon bayanta ta na rataye

da wata sharɓeɓiyar takobi a cikin kubenta, ta tunkaro inda dakarun suke babu alamun tsoro a tare da ita,
Al'amarin da ya yi matuƙar bawa dakarun mamaki kenan kuma ya ɗaure masu kai, domin tun da suke fitowa wannan ran-gadi hakan bai taɓa faruwa ba, da alamu wannan budurwa baƙuwa ce, amma koma dai baƙuwa ce ai ya kamata ace kwarjinin su ya firgita ta ?,
Amsar tambayar da dakarun suka kasa bawa kan su kenan,
Sa'adda da ya zama tazarar dake tsakanin su bata huce taku goma sai dakarun suka ja suka tsaya aka fara kallon-kallo tsakanin su da budurwar.

Daga can sai budurwar ta taka da ƙafafuwanta ta durfafi inda dakarun ke tsaye batare da fargabar komai ba, kafin dakarun su farga ta shammace su ta daga wawan tsalle ta dira a daf da wani badakare ta warce jakar dinaren dake hannunshi ta rataya a gadon bayanta, sannan ya dunƙule hannayenta biyu ta gabza mashi wawan naushi a wuya, nan take wuyan na shi ya ƙarye ya yi ƙara ruƙus! Kas, take ya faɗi ƙasa ko shurawa bai yi ba,
Ko da dakarun suka yi arba da abin da ya faru da Barde Ruhaizu sai suka firgita ainun, zukatansu suka kama tafarfasa tamkar za su ƙone.

Abin da ya firgita su ɗin shi ne shin ya aka yi budurwar ta samu irin gagarumin ƙarfi da ta kashe ɗaya daga cikin su bayan cewa tun da suke fitowa wannan ran-gadi hakan bai taɓa faruwa ba,
Abin da ya fusata su ɗin shi ne ta ya ya za a mace guda ɗaya jal! ta bayyana a gare su kuma har ta yi GABA DA GABA da su,
Lokacin da dakarun suka zo nan a tunanin su sai sai shugaba Shahral ya buɗe su ya dakama su tsawa dake nuna basu umarni su afkawa budurwar,
Cikin matuƙar fushi dakarun suka yi ɗauki izuwa gare ta suna ihu da kururuwa mai firgitarwa,
Ko da ganin hakan sai budurwar ta dunƙule hannayenta biyu ta gwara tsayuwa domin fafatawa,
Al'amarin da ya sanya shugaba Shahral ya bushe da dariyar mugunta kenan bisa ganin cewa budurwar ta yi wauta da ta kusanci mayakan ba tare da ta riƙe wani makami ba.

Lokacin da aka haɗu sai aka ruguntsume da azababban yaki mai matuƙar muni, Ban tsoro gami da tashin hankali,
Dakarun suka wanzu suna kai Budurwar sara da suka cikin matuƙar zafin nama juriya da bajinta,
Ita kuwa ta wanzu ta na zillewa hare-haren su cikin zafin nama gami da mayar da martani ta hanyar zabgawa dakarun naushi a sassan jikkunan su,
Duk inda ta nausa ɗin sai ka ga jini ya taru idan a baki ko hanci ne sai kaga yana yoyon jini,
Nan fa dakarun suka suka dinga zubewa ƙasa magashiyan.

Wohoho! Haƙiƙa duk wanda Allah ya ba shi jarumtaka ya more, kuma gaskiyar masu iya magana da suka ce "Duk wanda ya isa ya huta" inda a ce mutum yana tsaye a wannan waje lokacin da budurwar ke ragargazar dakarun tamkar tana sassabe a gonar audiga dole ne ya jinjina mata ya tabbatar da cewa ta cika JARUMAR ASALI.

Cikin abin da bai gaza daƙiƙa hamsin dakarun Shahral suka hargitsa kasuwar, domin duk sa'adda suka kaiwa budurwar hari da takubban su idan ta zillewa harin duk abin da takubban su suka sauka a kai sai ka ga ya yi bindiga ya tarwatse,
Rumfunan kasuwa kuwa a dinga rushe su ana bazar da su a ƙasa,
Nan fa jama'a suka shiga yin guje-guje gami da ifice-ifice domin TSIRA DA RAYUKAn si,

Lokacin da ya zamana an shafe tsawon rabin sa'a ana wannan ɗauki ba dadî sai ya zamana budurwar ta samu nasarar hallaka fiye kaso ɗaya bisa biyu na dakarun.

Sa'adda sadauki Shahral ya ga irin gagarumar ɓarnar da budurwar ke yi mashi sai ya fusata ainun ya dakawa sauran dakarun suka ja da baya, kawai sai ya dako wawan tsalle sama tamkar an harbo shi daga cikin baka yana saman ya zare waɗansu waɗansu zaratan takubba a gadon bayan shi ya kaiwa budurwar wawan hari da nufin tsinke mata wuya,

Cikin baƙin zafin nama zare takobinta ta kare harin,

Sannan suka ruguntsume da azababban yaƙi mai matuƙar muni, firgici da tashin hankali, Ana cikin wannan fafatawa ne sauran dakarun suka saci jiki suka fice daga kasuwar a bisa dawakansu suka kunna kai cikin gari tafiyar daƙiƙa hamsin kacal suka yi suka iso fadar birnin. Fadar ta kasance ƙasaitacciya da aka ƙawata ta da nau'ikan kayan more rayuwa, Gaba ɗaya ginin fadar an yi shi ne da waɗansu irin duwatsu masu ƙyalli tamkar gilashi, A wannan lokaci fadar ta cika maƙil da jama'a 'yan majalisa na zaune bisa ƙayatattun shimfiɗu na alfarma, kuyangi, Hadimai, Barori haɗe da dakaru na kai komo suna hidima.

Zaune bisa wata ƙasaitacciyar karagar mulki sarki Lamsarul-Azlam ne ya hakimce sanye ya ke cikin ƙayatattun tufafi na alfarma ya ɗora ƙafa ɗaya-kan-ɗaya ana gudanar da sha'anin mulki cikin annashiwa,

Sannu a hankali dakarun Sadauki Shahral suka shigo fadar lokacin da ya zamo tazarar dake tsakanin su da karagar mulki bai huce taku goma ba sai suka zube ƙasa suka kwashi gaisuwa wani cikin su ya buɗi baki cikin ladabi kanshi a sunukye ya yi gyaran murya ya ce " Ya shugabana bayan mun samu nasarar ƙarɓo jakar dinare daga hannun Sarkin kasuwa Isham kamar yadda muka saba sai mu ka yi gamo da wata hatsabibiyar jaruma har ta samu nasarar kwace jakar daga gare mu,

Kafin badakare ya gama rufe bakin shi Sarki Lamsarul-Azlam ya nuna badakaren da yatsan shi na hagu nan take wata irin gagarumar wuta ta kama ci a jikin shi nan badakaren ya shiga ihu da kururuwa, kafin cikar daƙiƙa ashirin ya ƙone ƙurmus,

Lamsarul-Azlam ya taƙarƙare ya kwarara ihu, daga bisani ya murtuke fuska tamkar an aiko mashi da Wasikar Mutuwa,

Sannan ya buɗe bakinshi ya shiga karanta waɗansu dalasiman tsafi, Ya na gama furta dalasiman sai ga wani shirgegen muridi ya bayyana a fadar,

Shi dai muridin yakasance mai matuƙar tsawo, kauri da kauri, yana da rafkeken kai mai ɗauke da manyan idanu jajaye tamkar garwashi, ƙofofin hancin shi manya ne tamkar mazirarin iska, Gaba ɗaya jikinshi cike yake da gashi buzu-buzu tamkar wani tsohon mahaukaci,

Haƙiƙa komai dakewar zuciyar mutum idan ya yi arba da muridin dole ya ɗimauce,

Sa'adda jama'a suka yi arba da muridin sai suka firgita ainun, amma saboda matuƙar tsoron sarki Lamsarul-Azlam sai kowanne ya zauna a wajen zaman shi cikin tashin hankali, Su kansu dakarun fadar a matuƙar razane suke,

Maridin ya zube ƙasa ya kwashi gaisuwa cikin girmamawa, Sarki Lamsarul-Azlam ya dube shi ya ce "Ya kai Zabratul-ukub ka yi sani cewa bakomai ne ya sanya na kirawo ka nan ba sai domin ina so ka tafi izuwa kasuwar dake cikin birni na inda dakaruna ke fafata yaƙi da wata jaruma ka dauko mani jarumar ina so ka kawo mani ita cikin ƙoshin lafiya".

Ko da jin wannan umarni daga bakin Lamsarul-Azlam sai maridi Zabratul-ukub ya ɓarke da wata irin mahaukaciyar dariya wacce ta bayyana wargatsattsun haƙoran shi marasa kyawun gani har wani irin taririn baƙin hayaƙi na fita daga cikin su,

A lokaci guda ya turɓune fuska cikin wata irin kakkausar murya mai kama da saukar aradu ya ce "Ya shugabana ai wannan aiki tamkar shaƙar numfashi ne a waje na na rantse da girman halarar tsafin ka zan kawo maka jarumar cikin ƙoshin lafiya,
Ko da gama faɗin hakan sai ya ɓace ɓat! tamkar bai taɓa wanzuwa ba,
Sarki Lamsarul-Azlam sai ya shiga ɓaɓɓaka dariyar mugunta tamkar ba zai daina ba.
Lokacin maridi Zabratul-ukub ya ɓace daga fadar sarki Lamsarul-Azlam bai bayyana a ko ina sai a wajen da shugaba Shahral ke fafatawa da kyakkyawar Budurwar nan,
A wannan lokaci budurwar ta samu nasarar hallaka haɗawa shugaba Shahral jini da majina sai layi ya ke yi jiri na ɗibar shi tamkar wanda ya sha barasa,
Sa'adda jama'a suka yi arba da maridi Zabratul-ukub sai suka fara cika wandon su da iska suna zurawa da gudun tsiya wasu har da sakin fitsari a wando saboda matuƙar tsoro, Kai hatta dakarun dake wajen ba a bar su a ba ya su ma dafe ƙeya suka yi suka sura da gudu domin a zaton su sarki Lamsarul-Azlam ya aiko da wata musiba domin ta hallaka kowa,
Kafin ƙiftawar ido babu kowa a filin kasuwar sai wannan kyakkyawar Budurwa,
Nan fa aka fara kallon-kallo tsakanin ta da Zabratul-ukub,
A iya tsawon rayuwar Budurwar bata taɓa ganin halitta mai muni da kwarjini tamkar wannan maridi ba, kawai dai ƙarfin hali ne irin na JARUMAR ASALI.
Sai da daƙiƙa talatin ta shuɗe ana wannan kallon-kallo tsakanin su tamkar ba za su afkawa juna ba,
Kawai sai Zabratul-ukub ya taƙarƙare ya kurma wawan ihu da ya firgita duk wata halitta dake birnin gidaje suka dinga rushe suna faɗawa kan al'umma suna hallaka, ba shiri kyakkyawar Budurwar ta sanya hannayenta ta tsohe kunnuwanta, tsawon daƙiƙa talatin ana cikin wannan hali sai daga bisani ne Zabratul-ukub ya tsuke bakinshi sannan komai ya samu dai-dai ta,
Kawai sai ya kaiwa budurwar cafka da hannunshi, cikin wani irin baƙin zafin nama budurwar ta daka tsalle gefe guda ta zillewa harin, abu kamar wasa sai ga shi budurwar ta tsallake harin shi fiye da goma,
Al'amarin da ya fusata shi kenan ya ce a cikin ran shi yanzu ace GWARZON ƘARNI tamka ta halitta guda ɗaya ta gagare ni tabbas wannan abun kunya ne,
Ko da ya zo nan a tunanin shi sai ya kawai ya shammaci budurwar ya ƙirɓa mata wani wawan naushi a fuska, saboda ƙarfin naushin sai da ta yi sama tamkar an janye ta da ƙungiya sannan daga bisani ta faɗo ƙasa tim! a matuƙar galabaice hancinta da bakinta na yoyon jini, har a wannan lokaci jakar dinaren da ta ƙarɓa daga hannun dakarun tana goye a gadon bayanta.
Ko da samun wannan gagarumar nasara sai maridi Zabratul-ukub ya bushe da dariyar farin ciki ya sanya hannunshi ɗaya ya ɗauki budurwar tamkar bil'adama ya ɗauki tuffa a tafin hannunshi, sannan ya ɓace ɓat! Tamkar bai taɓa wanzuwa ba,
Abin tambaya a nan shi ne daga ina wannan budurwa ta fito kuma mene ne dalilin da ya sanya ta kwace jakar dinaren dake hannun dakarun sarki Lamsarul-Azlam suka karɓo a wajen dattijo Isham,
Dalilin hakan kuwa shi ne Kamar haka:-

Mu haɗu a littafi na 6 domin jin cigaban wannan ƙayataccen labari.
Daga Mai ɗebe maku kewa a kullum da koyaushe.
MANSUR USMAN SUFI
Sarkin Marubuta Littattafan yaƙi
08137237071

TAFARKIN TSIRA
Rubuta Labari
MANSUR USMAN SUFI
Sarkin Marubutan Yaki
Wthapp Number
08137237071

BABI NA SHA ƊAYA

MADINATUL-AFNAN

Ƙasaitaccen birnin ya bunƙasa ainun a ƙarfin tattalin arziki, yawan al'umma gami da zaratan mayaƙa masu juriya a filin fama,
Gaba ɗaya jama'ar birnin suna da kyawawan halaye da mu'amala mai nagarta, hakan ya samo asali ne saboda kasancewar su ma'abota addinin musulunci,
Wannan al'amari ya janyo hankalin fatake daga sassan nahiyoyin duniya zuwa birin domin yin hulɗar siye da siyarwa, domin haka sai ya zamo tattalin arzikin birnin yana bunƙasa cikin ƙanƙanin lokaci kuma birnin ya zamo zarra a nahiyar,

Al'amarin da ya sanya biranen dake nahiyar suka kwallafa ran su akan ginin bayan birnin daga doron ƙasa amma Ubangiji baya ba su nasara.

Sarkin dake mulkin birnin yakasance dattijo ma'abocin kamala da sadaukantaka mutum ne mai son cigaban al'ummar shi ana kiran shi da suna RAYYAN IBN HUSSAIN Yana da matar aure guda ɗaya wacce ta haifa ma shi wata kyakkyawar 'ya da ake yiwa laƙabi da NUWAIRAT, Tabbas masu iya magana sun yi gaskiya da suka ce barewa ba za ta yi gudu ba ɗanta ya yi rarrafe,
Kamar yadda Sarki Rayyan yakasance GWARZON ƘARNI haka 'yarshi gimbiya NUWAIRAT ta kasance, domin a gaba daya birnin MADINATUL-AFNAN bayan sarki Rayyan babu jaruma tamkar ta, hatta kyawun halaye da tausayin al'umma Nuwairat ta gaji mahaifinta.

Tsakanin Sarki Rayyan da Sarki Lamsarul-Azlam ba a ga maciji ga juna, Lamsarul-Azlam ya zo ya kaiwa Rayyan harin bazato fiye da arba'in domin ya ga ya tunɓuke shi daga kan karagar mulki ya mallaki tarin arzikin dake birnin MADINATUL-AFNAN,
Wata rana sarki Rayyan na kwance a bisa gadon sarauta sai ya yi mugun mafarki daya sanya ya kasa rintsawa abin da ya gani a mafarkin shi ne sarki Lamsarul-Azlam ya na haɗa wani sinadarin tsafi wanda da zarar ya kammala zai samu nasara akan shi, sinadarin zai yi amfani da dukiyar da sarki Rayyan ke amfani da ita,
Bisa wannan dalili ya sanya sarki Rayyan ya umarci gimbiya NUWAIRAT ta tafi zuwa kasar Darul-Ashmar domin ta hana dakaru karɓar dinaren dake hannun sarkin kasuwa Isham,
Kuma a halin yanzu dinaren da gimbiya Nuwairat ta kwace daga hannun dakarun sune kaɗai suka rage wa sarki Lamsarul-Azlam ya mallaka domin kammala sinadarin tsafin.

***

Sa'adda Rusayyat uwar gidan shugaban 'yan fashin duniya sadauki fitinatul-Amir ta zurfafa izuwa kogin tunani domin samun mafita akan hanyar da zata shiga turakar mai gidanta ta ɗauko garin magani na sihiri, Domin ta tseratar da rayuwar Usaiba mai hatimin takobi, Sai ta shafe tsawon daƙiƙa talatin a cikin wannan hali ba tare da ta samu mafita ba,
Al'amarin da ya yi matuƙar dugunzuma hankalin ta kenan ta shiga damuwa ainun, Haka dai ta cigaba da nazarin daga bisani ne ta samu mafitar, ko da samun mafitar sai kawai ta miƙe tsaye zumbur daga kan kujerar da take zaune ta fita daga turakar ta nufi turakar mai gidanta,
Da yake a wannan lokaci safiya ce ko wane waje a gidan sarautar ya cika maƙil da barori, Hadimai da bayi, Duk inda Rusayyat ta gifta sai ka ga bayi da barori na zubewa ƙasa suna kwasar gai wawa cikin girmamawa, kai tsaye ɓangaren da ake dafa abinci ta kunna kai, sa'adda da kuyangi dake hidima a wajen suka yi arba da ita sai suka zube ƙasa suka kwashi gaisuwa, wata dattijuwa daga cikin kuyangin da ake kira da suna Ashrila ita ce ta yi gyaran murya ta ɗago da kanta cikin ladabi ta ce "Ya shugabata lafiya mu ka gan ki a wannan lokaci da ba ki saba zuwa ba ?
Ko da jin wannan batu daga bakin kuyanga  Ashrila sai Rusayyat ta daka mata tsawa ta dube ta ta ce "Ya ke Ashrila shin wane irin rashin hankali ne ya sanya ba a kai wa mai martaba uwan wanka kewaye ba, kuma an shirya abin kalaci har hasken rana ya bayyana haka?
Sa'adda Ashrila ta ji wannan tambaya sai jkinta ya kama tsuma yana ƙyarma saboda matuƙar tsoro bakinta na karkarwa ta ce " Ayi ma-ni afu-wa ya shu-gaba-ta"
"Ina so a kammala komai cikin daƙiƙa ashirin kacal!" Rusayyat ta faɗa sannan ta juya ta fice daga madafar ta nufi wata ƙofa ta musamman domin ta isa turakar mai martaba.

Lokacin da ta iso sai dakarun dake tsaron ƙafa suka zube ƙasa suka kwashi gaisuwa sannan suka wangame ƙofar ta kunna kai izuwa ciki, da shigarta ta tarar mai gidannata yana kwance bisa gadon sarauta yana sharar barci har da minshari,
Sai kawai ta matsa izuwa gareshi ta zauna a gefen gadon ta sanya hannayenta biyu ta shafi fuskar mai gidanta nan take ya farka ta hanyar buɗe idanuwanshi gami da yin miƙa ya zuba fararen idanuwanshi masu haske gami da kwarjini akan uwar gidant asa.
Cikin wani tattausan murmushi mai ɗimauta zuciyar duk wani ɗa namiji mai hankali cikin zazzaƙar murya mai daɗi tamkar sarƙewa ta ce "Barka da safiya SARKIN SADAUKAI ma'abocin kyawun sura da annuri, lafiya yau barcinka ya yi nauyi haka ?
Ko da jin wannan batu sai fitinatul-Amir ya yi murmushi mai kama da yaƙe ya ce "Tabbas kam yau na makara ya abar kaunata dare da rana kuma na yi mamakin hakan"
Rusayyat ta yi murmushi a karo na biyu sannan ta ce "Ya annurin rayuwata ai sai ka tashi ka shiga izuwa kewaye domin tuni kuyangi sun tanadi ruwan wanka"
Tana gama faɗin hakan sai ta miƙe tsaye tsam ta kama hannun mai gidanta ta tashe shi tsaye ta ja shi har izuwa inda kewayen ya ke sai da shigar da shi har ciki ta janyo Ƙofar ta rufe sannan ta dawo izuwa turakar ta shiga gudanar da bincike domin ta gano inda garin maganin shirin yake.
Abu kamar wasa sai ga shi Rusayyat ta shafe tsawon daƙiƙa hamsin ta na bincike a turakar amma ba ta gano inda garin maganin yake ba kuma a dai-dai a wannan lokaci ne ta jiyo alamun takun sawaye yana kusanto turakar, al'amarin da ya yi matuƙar dugunzuma hankalin ta kenan ta ta ji kamar ta saki fitsari a wando.

BABI NA SHA BIYU

A can Birnin Zainul-Ansar kuwa lokacin da aka cigaba da fafata azababban yaƙi tsakanin dakarun haɗin gwiwa da dakarun musulunci sai yazamana an rincaɓe MUTUWAR MAZAJE ihun dakaru gami da ƙarar karafniyar ƙarafa suka cika dodon kunne, sassan jikkunan bil'adama suka dinga shawagi a sama suna zuba a ƙasa JINI DA KASA suka cakuɗe babu kyawun gani.
A cikin gidan sarauta kuwa, sarki Nu'umanu da waziri Yazid sun wanzu suna kaiwa juna sara da suka cikin baƙin zafin nama JURIYA DAa BAJINTA, duk sa'adda takubbansu suka haɗu da juna sai ka ga tartsatsin wuta ya tashi haɗe da ƙara mara daɗin saurare,
Sai da suka shafe tsawon daƙiƙa hamsin a cikin wannan hali suna ɗauki-ba-daɗi amma ɗayansu bai samu nasarar lakutar jikin ɗan uwansa da takobinshi ba har makamansu suka fara dakushewa, yayin da sarki Nu'umanu ya ga abin da ke faruwa sai ya shiga neman taimakon Ubangiji a cikin zuciyarshi yana mai cewa "Ya Ubangijin halitta ka taimaki bawanka mai rauni a bisa maƙiyin addininka".
Tabbas! Ubangiji mai amsa roƙon bayinsa ne a duk lokacin da suka miƙa komai nasu izuwa gare shi,
Ana cikin wannan yaƙi ne sarki Nu'umanu ya samu nasarar yiwa waziri Yazid wani lafcecen sara a kafaɗarshi jini ya yi tsartuwa, kafin ya sake mayar da wani martanin waziri ya kaiwa masa wani bahagon sara a kafaɗarshi, duk da irin zafin naman da waziri ya yi wajen kaucewa saran sai da takobin ta yi masa rauni jini ya yi tsartuwa,

Kafin shudewar daƙiƙa talatin kowannensu ya yiwa abokin faɗanshi rauni fiye da guda goma layi na ɗibarsu tamkar waɗanda suka sha barasa suka bugu,
Al'amarin da ya yi matuƙar ɗaurewa Nu'umanu kai kenan kuma ba shi mamki bisa ganin cewa duk da yana neman taimakon Ubangiji amma ya gaza samun nasara akan abokin gabarshi, Abin da sarki Nu'umanu bai sani ba shi ne, kamar yadda yake neman taimakon Ubangijin Musulmi haka shi ma waziri ya ke yi.

Haƙiƙa masu iya magana sun yi gaskiya da suka ce "makashin ka yana nan tare da kai" kuma da zama da munafiki gwara zama da ɓarawo, domin shi dai munafiki yana tare da kai ne kuma yana cutar da kai ba tare da ka sani ba, shi kuwa ɓarawo sai ya ga kayanka zai ɗauka, yanzu dai ga shi Sarki Nu'umanu yana artabu da wazirinshi amma bai sani cewa shi ne abokin gabar shi ba,
Ana cikin wannan yaƙi ne sarki Nu'umanu da waziri Yazid suka cakawa junansu tsinin takubbansu a cinyoyinsu na hagu take wajen ya dare jini ya yi tsartuwa, a lokaci guda suka zube ƙasa magashiyan suna masu nishin wahala, a cikin wannan hali ne waziri ya shafi wani gurun tsafi a damtsenshi na dama ya ɓace ɓat! Tamkar bai taɓa wanzuwa ba,
A lokacinne waɗansu likitoci suka rugo izuwa wajen ɗauke da gado na ɗaukar mara sa lafiya aka shigar da shi izuwa cikin gidan sarauta domin ba shi taimakon gaggawa.

***

Al'amarin aljani Lattul-kifas kuwa, wato hadimin boka kaddadul-Gurub da ya tura domin farauto mashi yaro mai hatimin takobi domin ya yanka shi ya sha jinin shi,
Tun sa'adda ya kammala fafata yaƙi da dakarun dake gadin gidan shugaban 'yan fashin duniya ya kwanta barci, bai kwanta ba har sai da gari ya waye rana da ƙwalle sannan ya farka ya yi miƙa gami da hamma,
Sannan ya miƙe tsaye yana nazarin ƙofar da zai shiga gidan ko da kammala nazarin sai ya kaɗa fuka-fukanshi ya tunkari wani sashi, lokacin da ya rage saura taku goma ya isa ba sai kawai ya ji an ɗamƙe shi an shaƙama shi wani sinadari a hanci barci mai nauyi ya ɗauke shi, Bai tsinci kanshi a ko ina ba sai a cikin ƙasaitaccen kurkuku mai matuƙar kwarjini, duk inda ya kai dubanshi a kurkukun babu abin da zai gani face bayi, da barori na jinsin mutum da aljan suna ta kai komo suna aiyukan wahala waɗansu kuwa ana gana masu ukuba nau'i daban-daban.

Sa'adda aljani Lattul-kifas ya tsinci kanshi a cikin wannan kurkuku sai ya firgita ainun jikinshi ya kama tsuma bai sa'adda ya saki fitsari a wando ba, kawai sai ya yunƙura da nufin ya tashi sama, amma sai ya ji shi ɗaure cikin sasari na baƙin ƙarfe hannu da ƙafa,
Yana cikin wannan hali ne waɗansu irin samudawan dakarun aljanu biyu suka tusa ƙeyarshi izuwa wani ɗaki na musamman a kurkukun wanda aka gina shi da zallar duwatsun wuta masu ƙwarin gaske,
A tsawon rayuwar Lattul-kifas bai taɓa gani ko jin labarin kurkuku mai ɗauke da musibu da annoba tamkar wannan kurkuku ba,
Shi dai wannan kurkuku ana yi masa laƙabi da Sarirul-Maut, ma'ana matattarar dukkan musibun duniya, bokaye da masu hasashe sun tabbatar da cewa tun bayan rushewar kurkukun Sarkin bokayen duniya na farko wato boka shuyuɗan mai mallakin ANNOBA ƊARI ba a samu kurkuku mai ɗauke da musibu da nau'ikan azaba tamkar kurkukun Sarirul-Maut ba.

Ba wani ba ne ke ɗauke da mallakin kurkukun ba face sadauki fitinatul-Amir shugaban'yan fashin duniya, fiye da kaso hamsin na musibun dake kurkukun ya sana'anta su da ƙarfin shirin tsafi, kuma babu wata nau'in dabbar daji mai cutarwa da babu ita a cikin kurkukun, kuma a tarihin kurkukun ba a taɓa samun wani mahaluki da ya shiga kuma ya fito a raye ba.

***

Al'amarin sadauki ukaiza kuwa wato shugaban dakarun sarki Lamsarul-Azlam da ya tura domin farauto ma shi yaro mai hatimin takobi, sai da dare ya tsala sannan ya durfafi hanyar da zata sada shi da birnin Baitul-Ashmar, lokacin da ya zamana saura bai huce taku talatin tsakanin shi da birnin sai kawai ya yage wani yanki a tufafinshi ya rufe fuskarshi da shi ta yadda babu wanda zai iya gane shi, sannan ya durfafi ƙofar birnin,
Lokacin da dakarun dake tsaron ƙofa suka hango shi sai suka dafe kuben takubbansu domin jiran ko ta kwana,
Yayin da ya iso sai wani basamuden ƙato daga cikin dakarun wanda da alamu shi ne shugabansu ya dube shi da 'yan mini-minin idanuwanshi masu kama da garwashi saboda ja da suka yi ya dakama shi tsawa mai firgitarwa sannan daga bisani ya murtuke fuska tamkar an aiko mashi da WASIKAR MUTUWA cikin kakkausar murya ya ce "Shin wane ne kai? Kuma mene ne ke tafe da kai izuwa wannan birni namu mai albarka?
Ko da jin waɗannan tambayoyi sai ukaiza yayi shiru yana zurfafa cikin kogin tunani,
Abu na farko da ya faɗo mashi a rai shi ne shin yanzu zai miƙa wuya ne ga sarki Lamsarul-Azlam bayan cewa bai san halin da iyalanshi ke ciki ba?
Baka da wata mafita da huce ka yaƙi waɗannan dakaru domin ka isa inda iyalanka suke, ina amfanin ma miƙa wuya bayan baka da tabbacin ya lafiyarsu take.
Lokacin da Ukaiza ya zo nan a tunanin shi sai kawai ya kame bakinshi ya yi tsit! Ba tare da ya amsa tambayoyi da shugaban ƙafa ya yi masa ba,
Al'amarin da ya fusata sarkin ƙofar kenan ya dakawa yaransa tsawa dake nuna ba su umarnin su afkawa mashi,
Cikin hanzari suka zare makamansu suna ihu da kururuwa mai firgitarwa su ka yi ɗauki kanshi kafin da isa gare shi sai suka cika da matuƙar mamaki, abin da basu mamaki shi ne yadda tsananin yawan su bai firgita baƙon ba tabbas wani sirri game da shi domin Ruwa baya tsami banza! Kuma idan ka ji makaho ya ce ayi wasan jifa to yaji ya taka dutse!
Lokacin da ya rage saura taku uku tsakaninsu sai Ukaiza ya zare wata sharɓeɓiyar takobi a damtsenshi ya yi wata irin katan-tanwa a ƙasan dakarun take ya sare mutum goma ƙafafu suka zube ƙasa guragu suna masu kurma wawan ihu,
Sannan ya afkawa sauran aka ruguntsume da azababban yaƙi mai matuƙar muni ban tsoro daban al'ajabi.

Mu haɗu a TAFARKIN TSIRA littafi na 7 domin jin cigaban wannan ƙayataccen labari.
Daga mai ɗebe maku kewa a kullum da koyaushe.
MANSUR USMAN SUFI
Sarkin Marubutan Yaki

08137237071

TAFARKIN TSIRA 7
Rubuta Labari
MANSUR USMAN SUFI
Sarkin Marubutan yaƙi
Wthapp Number
08137237071

ELEGANT ONLINE WRITER'S

Littafan Marubucin

Kogon Annoba
Sarautar Mutuwa
Kangin Bauta
Jaruman Duniya
Takobin Ɗaukaka
Ƙarshen Zalunci
Fataucin Bayi
Sarkin Sadaukai
Goga Sha Fama
Tafarkin Tsira
Gasar Sarauta
Kundin Al'ajabi

BABI NA SHA UKU

Sa'adda muridi Zabratul-ukub ya samu nasarar ɗaukar wannan kyakkyawar dudurwar da ta fafata yaƙi da dakarun sarki Lamsarul-Azlam, kuma ya ɓace ɓat! Cikin alƙalumman sihiri, yana cikin wannan hali ne sai ya ji jikin shi ya ɗauki zafi, ba shiri ya bayyana ba a tsakiyar wani makeken fili mai ɗauke da rairayi, yana sauka sai ya duba tafin hannunshi aikuwa sai ya gan shi wayam babu wannan kyakkyawar dudurwa, cikin hanzari ya ɗaga kanshi izuwa sararin samaniya nan take ya yi arba da wani kyakkyawan aljani ɗauke wannan kyakkyawar dudurwa wato gimbiya NUWAIRAT yana tsala gudu a sararin samaniya, kafin ƙiftawar idanu ya ɓace ɓat tamkar bai taɓa wanzuwa ba,

Cikin matuƙar takaici Zabratul-ukub ya ya taƙarƙare ya kurma wawan ihu, a lokaci guda kuma ya turɓune fuska, sannan ya sake ɓacewa a karo na biyu bai bayyana a ko ina ba sai a tsakiyar fadar sarki Lamsarul-Azlam ya zube ƙasa ya kwashi gaisuwa kanshi a sunkuye,
Lamsarul-Azlam ya daka ma shi tsawa wacce ta sanya hantar cikin kowa dake fadar ta kaɗa saboda matuƙar tsoro, a lokaci guda ya turɓune fuska tamkar an aiko ma shi da WASIƘAR MUTUWA cikin kakkausar murya ya ce "Ya kai Zabratul-ukub shin wane irin rashin hankali ya sanya har ka yi sake gimbiya Nuwairat ta suɓuce daga hannunka ? Tabbas ka aikata babban kuskure a gare ni, na rantse da girman halarar tsafina sai na gana maka nau'ikan ANNOBA ƊARI wacce ba a taɓa yiwa wani mahaluki ita ba.

Ko da gama faɗin hakan sai ya nuna Zabratul-ukub da ɗan yatsanshi na hagu take nan take waɗansu irin sarƙoƙin wuta suka ɗaure shi hannu da ƙafa, nan fa ya shiga yin kururuwa da neman agaji saboda yadda sarƙoƙin ƙe ƙona sassan jikinshi,
Al'amarin da ya firgita Al'ummar fadar kenan kuma cikin ya ɗuru ruwa, waɗansu har suna sakin fitsari a wando,
Sa'adda Zabratul-ukub ya ga cewa a koda yaushe zai iya rasa rayuwarshi sai ya shiga yin magiya yana roƙon sarki akan ya cewa idan har ya ƙyale shi zai kirawo dukkan jinsinsu na muridai su je su yaƙi gaba ɗaya jama'ar birnin MADINATUL-AFNAN ko da kiyashi ba za su bar shi a raye ba,
Ko da jin wannan magajiya sai sai sarki ya yi nuni gare shi a karo na biyu take sarƙoƙin suka ɓace ɓat! Daga jikinshi tamkar ba su taɓa wanzuwa ba,
Sannan ya dube shi ya ce "Ka sani cewa kwanaki uku kacal na ɗaukar maka idan har aka samu matsala kafi kowa sanin abin da zai biyo baya,"
Cikin ladabi da ƙasƙantar da kai Zabratul-ukub ya ce muryarshi na rawa "Godi-ya na-ke ya ma-i du-ni-ya",
Yana gama faɗin hakan ya shafi shimfiɗar fadar ya sake ɓacewa a karo uku tamkar bai taɓa wanzuwa ba.

A sannanne jama'a suka dawo cikin hayyacin su, shiru ne ya wanzu a fadar tamkar an yi ruwa an ɗauke, daga can sai sarki ya katse shirun da ya wanzu ta hanyar buɗar baki ya dubi sarkin yaƙi ya ce "Ya kai dirkar birnina ka yi sani cewa ina so ka fara shirye-shiryen fita yaƙi ina so alfijir ɗin kwana biyu masu zuwa ya keto a lokacin da muke tsaye a ƙofar birnin MADINATUL-AFNAN, domin wannan yaƙi da zamu fita ya bambanta da sauran yaƙoƙi, domin dole ka haɗa mana rundunar KARE DANGI,
Ko da sarkin yaƙi Huzmal ya ji wannan batu sai ya risina ya ce "An gama ya shugabana yaba gama faɗin hakan ya miƙe tsaye tsam! Daga kan kujerarshi ya durfafi ƙofar fita daga fadar,
Kallo ɗaya zaka yiwa Sarkin yaƙi ka fahimci cewa ya cika gwarzon Jiya, domin ya tara ƙwanji, kwarji da Haruna, komai dakewar zuciyar jarumi idan ya yi arba da shi sai hantar cikinshi ta kaɗai,
Ko da ficewar shi sai sarki Lamsarul-Azlam ya tafi ya shiga izuwa gidan sarauta dakaru na take masa baya, nan take fadar ta watse kowa ya kama gabanshi tamkar wata halitta bata taɓa wanzuwa ba.

***

Lokacin da Rusayyat ta ci gaba da gudanar da bincike a turakar maigidanta sadauki fitinatul-Amir domin ta gano wannan garin magani na sihiri don tseratar da rayuwar yaro Usaiba

mai hatimin takobi, lokacin da ta ji alamun takun sawaye na tunkaro turakar, sai kawai ta miƙe tsaye zumbur! Ta ruga izuwa bakin ƙofar shigowa ta sanya idanuwanta a tsakiyar wata 'yar siririyar ƙofa dake jikin ƙofar, nan take ta hango cewa ashe wata kuyanga ce ɗauke da wani ruwa a cikin kasko, nan take ta cika da matuƙar farin ciki, jim kaɗan ƙofar ta buɗe, Rusayyat ta dakawa kuyangar  tsawa cikin matuƙar fushi ta dube ta ta ce "Ya ke Hulaifa shin mene ne ya kawo ki nan ? Bayan cewa an kawo dukkan abin da na buƙata ?
Ko da jin wannan tambaya sai jikin Hulaifa ya kama kyarma ta buɗi baki cikin ladabi ta ce "Ki gafarce ni ya shugabata na manta ne ba a kawo ruwan ɗauraye hannu ba ne, shi ne yanzu na kawo",
"Bama buƙatar komai yanzu".
Rusayyat ta bata amsa.
Hulaifa ta risina sannan ta juya ta fice daga turakar, dakarun dake tsaron ƙofar suka sake kulleta,
Kawai sai Rusayyat ta koma izuwa cikin turakar ta cigaba da binciken cikin hanzari, cikin sa'a ta samu nasarar gano garin maganin, cikin matuƙar farin ciki maral-musaltuwa ta sanya shi a cikin aljihun rigarta na hagu, sannan ta sanya hannunta a aljihun na dama ta ɗauko hodar banju ta taka da ƙafafuwanta izuwa wajen da teburin abinci yake ta buɗe kofin dake ɗauke da taceccen ruwan inibi ta zuba a banjun a ciki, sannan ta mayar ta rufe ta zauna a ɗaya daga cikin ƙayatattun kujerun dake wajen.
Jim kaɗan da aiwatar da hakan sai ƙofar da ke ɓangaren yamma a turakar ta buɗe sai Fitinatul-Amir ya bayyana sanye cikin tufafin alfarma irin na hamshaƙan sarakai, wani irin daddaɗan ƙamshi na tashi a jikinshi,
Haƙiƙa shigar ta yi matuƙar fito da tsantsar kyawunshi, domin babu wata mace da za tayi arba da shi a cikin wannan yanayi face ta kamu da matuƙar ƙaunarshi,
Yayin da Rusayyat tayi arba da shi sai miƙe tsaye tsam! Ta tare shi suka rungume juna na tsawon daƙiƙa goma, sannan Fitinatul-Amir ya janye jikinshi daga nata, sannan ya ja hannunta har izuwa inda teburin abincin yake suna zaune a bisa kujerun,
Ba tare da wani jinkiri ba suka shiga kimtsa cikinsu suna fira cikin nishaɗi da tsantsar soyayyar juna, cikin matuƙar farin ciki Rusayyat ta ɗauki kofin da ta zuba wannan banju a cikin shi ta sanya wa mai gidanta a bakinshi ya shiga kwankwaɗar ruwan har sai da ya sha ya ƙoshi,
Bayan sun kammala kalacen ne Rusayyat ta lura idanuwan mai gidanta sun fara lunshewa, sai ta dube shi cikin tattausan murmushi mai ɗimauta zuciyar masoya ta ce "Ya uban 'ya'yana lafiya kuwa na ga alamun ɓarci a fuskarka?
Koda jin wannan tambaya sai Fitinatul-Amir ya yi murmushi a gare ta sannan yace " kwarai kuwa zancenki duste ya abar kaunata, haƙiƙa ina jin barci mai nauyi sosai, koda gama faɗin hakan sai ya miƙe tsaye tsam! Ya kama hannun Rusayyat suka nufi wani ƙasaitaccen gado a turakar ya kishingiɗa akai, kafin Rusayyat ta yi wani yunƙuri har ya fara aikin rago idanuwanshi sun rufe,
Cikin matuƙar farin ciki maral-musaltuwa Rusayyat ta miƙe tsaye zumbur! Ta fice daga turakar, Kai tsaye turakar su yaro Usaiba ta nufa, duk inda ta gifta a gidan sarautar sai dai kaga dakaru, kuyangi, da bayi ba zubewa ƙasa suna kwasar gaisuwa,
Lokacin da ta shiga turakar ta su sai ta iske har yanzu barci suke yi ba su farka ba, cikin matuƙar farin ciki ta ɗauki garin magani na farko ta buɗe gadon bayan yaro Usaiba ta shafa masa, nan take zanen hatimin takobin Saiful-zayyad ya ɓace ɓat! Tamkar bai taɓa wanzuwa ba,

Sannan ta buɗe bakinta ta karanta dalasiman tsafi ta tofa akan garin magani na biyu wanda shine kaɗai zai iya ƙarya shirin zanen hatimin takobin ya bayyana, tana gama rufe bakinta garin maganin ya ɓace ɓat tamkar bai taɓa wanzuwa ba,
A sannanne ta ja wata doguwar ajiyar zuciya, kuma ta ƙurawa Yaro Usaiba da 'yar uwarshi Hairat idanu hawayen farin ciki suna kwaranyo mata,
Domin a halin yanzu ta samu nutsuwa a zuciyarta tun da ta tseratar da rayuwar yaro Usaiba mai hatimin takobi daga sharrin mai gidanta shugaban'yan fashin duniya dake farautar shi dare da rana domin ya hallaka shi,
Wannan shi ne abin da ya faru da Jaruma Rusayyat da mai gidanta Sadauki Fitinatul-Amir.

Lokacin da lokacin birnin Zainul-Ansar suka ɗauki sarki Nu'umanu bisa ƙasaitaccen gadon marasa lafiya suka shiga da shi izuwa cikin gidan sarauta, sai suka huce kai tsaye da shi izuwa turakarshi suka shimfiɗe shi suka shiga duba lafiyar shi, suka ɗinke duk wani rauni dake jikinshi aka sanya masa magani, wani abu da ya bawa likitocin mamaki shine, duk da sarki Nu'umanu yana cikin halin jinya amma bakinshi bai gushe ba wajen ambaton Allah da yiwa annabin shi Salati.

Cikin abin da bai gaza daƙiƙa hamsin likitocin suka kammala aikin su, kawai sai wani dattijo ma'abocin haiba daga cikin likitocin ya ɗauki wani ruwan magani dake cikin kofin azurfa ya sanya hannunshi ɗaya ya tashi kafaɗun sarki domin ya ba shi maganin, amma sai sarki ya dakatar da shi ta hanyar ɗaga mashi hannu da yake yi mashi nuni ya dakata, sannan ya buɗi baki muryarshi na sarƙewa ya ce " Ya kai likita sha'aban kayi sani cewa bana buƙatar a shayar dani maganin da zai sanya ni barci domin lokacin sallah ya yi har a alfijir ya keto,
Zai fi kyau a ƙyale shi sai na yi sallah sai na sha,
Koda jin wannan batu daga bakin sarki sai likita sha'aban ya gyaɗa kai yana jin ƙaunar sarki a zuciyarshi domin kuwa ya tabbata cewa shi shugaba ne abin koyi,
Batare da wani ɓata lokaci ba sarki ya yi kabbara ya tayar da sallah yana da kwance, yana mai rufe idanuwanshi gami da ɓudewa kuma bakinshi yana motsi alamun cewa ya fara gabatar da sallar, jin kaɗan ya ya sallama, sannan likita sha'aban ya ba shi ruwan maganin a baki ya kurɓe,
Har wani daga cikin likitocin wani kyakkyawan saurayi ya buɗi baki cikin matuƙar mamaki domin ya ce wani abu amma sai sha'aban ya tari numfashi shi ya dube shi fuskarshi cike da annuri ya ce " Yakai Sultan ka yi sani cewa na san ba wata tambaya kake da bukatar kayi mani ba face yadda sarki ya gudanar da inadarshi,
To ina so ka yi sani cewa addini ya sanya sallah ta zamo wajibi ga dukkan Musulmi matsawar hankalinshi bai gushe ba, a kowa ne irin yanayi mutum zai iya yin Sallah, saboda muhimmancin sallah Annabi SAW da Sahabbanshi a yaƙi suka yi sallah, ka ga kenan da Allah zai ɗaukewa wani da ya ɗaukewa Annabin shi SAW da Sahabbanshi",
Koda jin wannan bayani daga bakin likita sha'aban sai Sultan ya jinjina kai alamar gamsuwa,
Ana cikin wannan hali ne aka jiyo motsi na kusanto turakar cikin hanzari kowa ya waiga domin aga ko wane ne, kawai sai aka yi arba da gimbiya lawisat,
Domin sai likita sha'aban da muƙarrabanshi suka juya suka fice daga turakar cikin hanzari,
A dai-dai lokacin lawisat ta iso daf da gadon da sarki ke kwance fuskarta cike da alamun matuƙar damuwa.

Wannan shi ne abin da ya wakana a cikin gidan sarautar birnin Zainul-Ansar.

BABI NA SHA HUƊU

Al'amarin waziri Yazid kuwa tun sa'adda ya ɓace ɓat! Bayan ya kammala fafata BAƘIN ARTABU da sarki Nu'umanu, bai bayyana a ko ina ba sai a cikin gidan sarautar a cikin wata ƙasaitacciyar turaka sarki Rakibu, cikin hanzari likitoci suka taru a kan shi domin ba shi taimakon gaggawa, cikin abin da bai gaza daƙiƙa talatin ba likitocin suka kammala aikin su, jim! Kaɗan da ficewar likitocin sai sarki Rakibu da sarkin yaƙi suka shigo turakar suka samu kujeru suka zauna dake fuskantar waziri Yazid fuskokinsu cike da matuƙar damuwa tsawon daƙiƙa goma babu wanda yace ƙala a cikin su,
Sai daga can sarki Rakibu ya katse shirun da ya wanzu ta hanyar buɗe baki ya ce " Ya waziri shin mene ne mafita ? Ga shi yanzu haƙan mu bai cimma ruwa ba duk shirin da mu ka yi akan sarki Nu'umanu da jama'ar ya tashi a banza",
Koda jin wannan batu daga bakin Rakibu sai waziri cikin sarƙewar murya ya ce " Ya ku manyan abokai na ku yi sani cewa ba a san MAZAN JIYA da tsoro ba, rashin nasara akan abu shi ne ke nuna alamun nasarar, domin rashin nasara shi ne zai sanya ka gyara kusakuren da ka aikata, ku yi sani cewa matuƙa kuka bi waɗansu sharuɗɗa da zan gindaya tabbas nasara ta same mu.
Da farko dai wajibi ne mu nemo ZARATAN JARUMAI da suka ƙware ainun a leƙen asiri da za su dinga kawo mana rahoton shirin abokan gabarmu,
Sannan zan sihirce wani hadimana domin ya kasance mai sura irin tawa zai tafi zuwa ga sarki Nu'umanu a matsayin cewa ni ne, wannan wata hanya ce da zata ɗauke hankalin sarki Nu'umanu da sauran al'ummarsa akan gano cewa da ni za a ci amanar su,
Sannan zamu nemi taimakon waɗansu daga cikin GWARAZAN JARUMAI na jin MUTUM DA ALJAN,
Sa'adda sarki Rakibu da sarkin yaƙi suka ji wannan dogon jawabi daga bakin waziri sai suka cika da matuƙar farin ciki maral-musaltuwa,
Amma Rakibu ya buɗi baki ya dubi waziri ya ce "To amma ba ka tunanin cewa idan aka samu gawarwakin dakarunmu za a gano cewa mu ne muka kai MAMAYAR BAZATO ?,
Da jin wannan batu sai dariya ta suɓucewa waziri ya dube shi ya ce " Ya kai Rakibu ban da abin ka ai lokacin da muka ɓace daga birnin Zainul-Ansar bayan ARTABU ai tare da gawarwakin dakarunmu muka tawo,
Lokacin da yazo nan a zancen shi sai mayar da duban shi ga sarkin yaƙi sannan ya ɗora da cewa,
Kai kuma sarkin yaƙi za ka koma birnin Zainul-Ansar ka zauna tare da sarki Nu'umanu a zahiri za ka nuna kana tare da shi amma a baɗini ba haka ba ne za ka dinga bawa 'yan leƙen asirinmu bayanai ne kawai,
Da jin wannan ƙarin bayani sai dariyar farin ciki ta suɓucewa sarki Rakibu,
Ba tare da ɓata lokaci ba waziri ya ƙwallawa hadimin sa kira, jim kaɗan! Ya bayyana gare shi ya zube ƙasa ya kwashi gaisuwa,
Kawai sai waziri ya nuna shi a ɗan yatsanshi na hagu tare da karanta waɗansu dalasiman tsafi yana gama rufe bakinshi nan take siffar hadimin ta koma san! Ta waziri Yazid tamkar an tsaga kara, su kansu su sarki Rakibu sai da tunanin su ya dagule suka kasa tantance waziri na gaskiya da na bogi,

Faruwar hakan ke da wuya sai waziri ya sake nuna hadimin da yatsanshi na hagu a karo na biyu take ya ɓace ɓat! Tamkar bai taɓa wanzuwa ba,
Sannan ya yi nuni izuwa ga bangon turakar sai ga taswirar turakar sarki Nu'umanu ta bayyana yana kwance bisa gadon sarauta uwar gidansa Lawisat na zaune a gefen shi cikin alamun matuƙar damuwa, suna cikin wannan hali ne wannan hadimi mai ɗauke da siffa irin ta waziri ya shigo turakar hankalin shi ya yi matuƙar DUGUNZUMA,
Koda ganin wannan taswira sai sarki Rakibu, Sarkin yaƙi da waziri Yazid suka bushe da dariyar mugunta har da ƙyaƙyatawa.

Al'amarin gimbiya Nuwairat kuwa tun sa'adda ta suɓuce daga hannun muridi Zabratul-ukub cikin halin suma, wannan hadimin aljani ma'abocin kyawun sura ya ɗauke ta bai tsaya ko ina sai birnin MADINATUL-AFNAN,
Lokacin da sarki Rayyan ya ga halin da gimbiya ta ke ciki sai hankalinshi ya DUGUNZUMA ainun ya tura wata kuyanga ta kirawo mashi liktar masarautar mai suna karima,
Karimat ta bayyana a gare shi tare da mataimakanta suka zube ƙasa suka kwashi gaisuwa cikin girmamawa,
Cikin hanzari karima da sauran likitocin suka nufi gadon da aka kwantar da gimbiya suka shiga ƙoƙarin ceto rayuwarta, koda ganin hakan sai sarki Rayyan ya ɗauke jakar dinaren dake ajiye ajiye a gefen Nuwairat ya juya ya fice daga turakar cikin alamun matuƙar damuwa,
Kai tsaye harabar turakarshi ya nufa ya dinga kai-komo ya kasa zaune,
Yana cikin wannan hali ne sarkin yaƙi Zubairu ibn Saiful-Zaman ya bayyana a gare shi,
Sarkin yaƙi yakasance GWARZON KARNI mai tarwatsa DANDAZON MAYAƘA a FILIN FAMA, kyakkyawa ne na gaban kwatance wanda ganin farko zai ɗimauta zuciyar duk wata 'ya mace mai hankali, ya gaji sarautar sarkin yaƙi ne a wajen mahaifinshi Barde Huburul-zaman,
Ya jagoranci yaƙoƙi guda ashirin da uku kuma duk ya samu nasara,
Bisa wannan dalili yasanya sarki Rayyan ya ja shi a jikinshi duk wani abu nashi ya ke sanya shi a ciki,
Tsakanin sarkin yaƙi da gimbiya Nuwairat akwai soyayya mai ƙarfi sai dai sun gaza bayyanawa,
Sarkin yaƙi ya yi sallama irin ta ma'abota addinin Musulunci gami da risinawa ƙasa ya kwashi gaisuwa,
Sarki Rayyan ya amshi gaisuwar tare da miƙa mashi hannu suka yi musabaha, kuma ya ja hannunshi har izuwa bisa kan wata ƙasaitacciyar kujera suka zauna tare sannan ya dube shi cikin nutsuwa ya ce " Ya kai dirkar birnin MADINATUL-AFNAN kayi sani cewa bakomai ya sanya na kirawo ka nan ba sai domin na bayyana maka cewa gimbiya Nuwairat ta samu nasarar ɗauko jakar dinaren dake hannun abokin gabarmu sarki Lamsarul-Azlam gani tare da shi ya kare batun yana miƙa mashi jakar ya ƙarba sannan ya ɗora da cewa " Wannan nasara da muka samu ba za ta saka mu saki jiki ba, domin a kowa ne lokaci abokan gaba za su iya kawo mana MAMAYAR  BAZATO, domin haka wajibi mu tanadi dakarun kar-ta-kwana",
Koda jin wannan jawabi daga bakin sarki Rayyan sai sarkin yaƙi ya buɗe baki cikin ladabi ya yi gyaran murya ya ce " Ya shugabana na ji dukkan bayanin ka kuma da yardar Allah SWT za a aiwatar da komai yadda ka buƙata, sai dai ranka ta daɗe shin ko a wane hali gimbiya take ciki? Ya ƙare batun cikin alamun damuwa,

Sarki Rayyan ya yi murmushi mai taushi a gare shi ya dafa ƙafadunshi da hannayenshi biyu ya ce " Kar ka damu ta ɗan samu buguwa ne a kan ta likitoci suna can suna bata kulawa zata samu lafiya",
Da jin amsar wannan tambaya sai Zuhairu ya risina ga sarki ya miƙe tsaye ya fice daga harabar hannunshi ɗauke da wannan jakar dinaren.
Wannan shi ne abin da ya faru a can birnin MADINATUL-AFNAN bayan farin hadimin aljani ya samu nasarar ceto gimbiya Nuwairat daga hannun muridi Zabratul-ukub.

TAFARKIN TSIRA 8
Rubuta Labari
MANSUR USMAN SUFI
Sarkin Marubutan Yaƙi
Wthapp Number
08137237071

ELEGANT ONLINE WRITER'S

Littafan Marubucin

Kogon Annoba
Sarautar Mutuwa
Kangin Bauta
Jaruman Duniya
Takobin Ɗaukaka
Ƙarshen Zalunci
Fataucin Bayi
Sarkin Sadaukai
Goga Sha Fama
Tafarkin Tsira
Gasar Sarauta
Kundin Al'ajabi

BABI NA SHA BIYAR

A can gidan sarautar shugan 'yan fashin duniya sadauki fitinatul-Amir kuwa, lokacin da yaro Usaiba mai hatimin takobi da 'yar uwarshi Hairat suka farka daga barci sai kuyangi suka shiga da su kewaye suka yi masu wanka suka sanya masu tufafi masu tsadar gaske, bayan an shirya masu abin kalaci sun kimtsa cikinsu sai Rusayyat ta ɗauke su a bisa wani ƙayataccen keken doki ta shiga da su izuwa lambun shaƙatawa ta zaunar da su ƙarƙashin wata itaciya mai manyan rassa,
Lambun ya ƙawatu da nau'ikan shuke-shuken furanni masu kyawun launi da ƙamshi, ƙoramu na gudana da ruwa garai-garai, waɗansu irin tsuntsaye masu kyawun launi da kuka mai daɗin saurare ya shawagi a rassan bishiyu,
Wohoho! Haƙiƙa wannan lambu ya cika aljannar duniya, domin babu wata halitta a doron ƙasa MUTUM DA ALJAN da za su tsinci kansu a wannan waje face sun ƙwadaitu da su kasance a lambun har ƙarshen rayuwar su.
Shiru ne ya wanzu a tsakanin su na ɗan lokaci daga bisani Yaro Usaiba ya katse shirun da wanzu ta hanyar ɓudar baki ya yi gyaran murya ta ce " Ya ummun mu kin yi mana alkawari cewa za ki bamu labarin rayuwarki?.
Koda jin wannan tambaya sai ƙwalla ta zubo daga idanun Rusayyat,
Al'amarin da ya yi matuƙar DUGUNZUMA hankalin Usaiba da 'yar uwarshi kenan ya dube ta cikin alamun matuƙar damuwa ya ce " Ya ummina ki yi mini afuwa idan tambayar da nayi miki ta ɓata maki rai",
Rusayyat ta yi guntun murmushi a gare shi ta buɗi baki a karo na farko ta ce " Ko kaɗan tambayar ka bata ɓata mini rai ba, kawai dai ta tuna mini da labarin uƙubar da na sha a rayuwata,
Yanzu sai ku gyara zama domin ku ji yadda labarin nawa ya kasance.
Rusayyat ta fara labarin kamar haka:-

A wani zamani can baya mai tsawo da ya shuɗe a yankin ƙasashen Larabawa an yi wani ƙasaitacciyar birni da ake yiwa laƙabi da Hairul-Mazwar,
Birnin Hairul-Mazwar ya bunƙasa ya bunƙasa a arziƙin noma da kiyo, suna da ZARATAN JARUMAI masu juriya a FILIN DAGA, har su fatake ke kiran sunan da suna BIRNIN SADAUKAI,
Sarkin dake mulkin birnin ana yi mashi laƙabi da Hubru ibn Kamsil,
Sarki Hubru yakasance dattijon mutum mai tausayi da jin ƙari, GWARZON MAYAKI ne mai tarwatsa DANDAZON JARUMAI a filin fama,
Bisa wannan dalili yasanya sarakunan dake maƙwabtaka da shi suke matuƙar shayin shi, Ni da mahaifana muna zaune ne a ƙauyen da ke wannan birni, kasancewar mu talakawa hakan yasanya bana samun wani jin daɗin rayuwa sosai,
Mahaifina yakasance makaho, mahaifiyata kuwa gurguwa ce bata da ƙafafu, a kowa ce hudowar rana ni da mahaifana sai mun shiga izuwa cikin birni mun yi bara, abin da muka samu da shi za mu yi kalaci, duk ranar da ba mu samu ba kuwa sai dai mu kwana da yunwa.
Wata rana ni da mahaifana muna bara a cikin kasuwa ina riƙe da sandarshi, sai mu ka zo hucewa ta rumfar wani attajiri,

Attajirin yakasance garjejen ƙato, fuskarshi mai matuƙar gwarjini ce yana da idanuwa jajur! Tamkar garwashi ya tara ƙasumba da gemu mai tsawo da ya shimfiɗo har bisa ƙirjinshi, kanshi a salsale yake babu ɗigon gashi ko ɗaya sai ƙyalli yake yi tamkar sabuwa tasa,
Kallo ɗaya za ka yi masa ka fahimci cewa yana da ƙarfi na Allah ya isa, kuma ya tara dukiya mai tarin yawa saboda surutan dake sanye a jikinshi irin na hamshaƙan sarakai ne, kai ! Ko takalmi da kwamitin dake hannunshi abin kallo ne,
Har mun huce ta gaban attajirin sai ya kirani na zo na ƙarɓi sadaka, cikin matuƙar farin ciki ya ja sandar mahaifana da nufin na koma da baya domin tun da muka baro gida babu wanda ya bamu koda dinare guda amma bisa mamaki sai na ji mahaifana ya tsaya can! Ba tare da motsa daga inda yake ba, a tunani na ko bai fahimci abin da nake nufi ba ne sai kawai na ƙyale shi anan tsaye na nufi inda wannan attajiri ke hakimce a cikin rumfarshi,
Tun kafin na iso gare shi ya ƙura mini idanu ko ƙiftawa ba ya yi, kuma fuskarshi cike da annuri tamkar wanda aka bawa SARAUTAR DUNIYA,
Lokacin da na isa gare shi sai ɗebo dinare mai tarin yawa a cikin wata jakar fata ya miƙa mini cikin ladabi hannayena na kyarma saboda mamakin yawan dinaren wanda sai mu shekars muna bukatunmu da shi na durƙusa na ƙarɓa, sannan ya koma izuwa inda a bana ke tsaye na riƙe sandar jagora mu ka cigaba da tafiya,
Muna cikin wannan tafiya ne na waiga izuwa inda wannan attajiri yake aikuwa sai na ga har yanzu bai ɗauke idanuwanshi daga kaina ba,
Nan take n tambayi kaina a cikin raina na ce shin wannan attajiri tsananin tausayin da yake yi mana ne yansa shi wannan murmushi ko kuwa? Kuma na lura da yadda fuskar abbana ta canza a cikin ƙanƙanin lokaci,
Amsar tambayar da ba kasa bawa kaina kenan,
Kawai na dubi mahaifina cikin alamun matuƙar damuwa na ce " Ya abbana shin ina dalilin wannan fushi na ka? Shin baka farin ciki bisa wannan sadaka da muka samu da za ta iya magance mana dukkan matsalolinmu na rayuwa ?
Koda jin wannan tambaya sai abbana ya sake murtuke fuska al'amarin da ya sanya na sha jinin jikina keman,
Daga bisani ya yi ajiyar zuciya ya dube ni ya ce " Ya cikar muradin rayuwa ta kiyi sani cewa da ace kin san abin da na sani da ba kiyi gangancin ƙarbar sadakar wannan attajiri ba, domin babu wani alkairi a tare da shi,
Ina mai baƙin cikin sanar da ke cewa a halin yanzu rayuwarmu na cikin halin TSAKA MAI WUYA wajibi ne a gare mu mu yi hijira daga su tafi izuwa wata nahiyar domin shirya wa kan mu sabuwar rayuwa",
Koda jin wannan batu sai hankalina ya DUGUNZUMA ainun na dubi mahaifana cike da matuƙar mamaki na ce " Ya abbana shin mene ne sharrin da ka sani a tare da wannan attajiri da har zai sanya mu yi hijira ?,
Mahaifina ya gyaɗa kai cikin takaici ya ce " Ya 'yata ki yi sani cewa a halin yanzu babu lokacin da zan iya bayyana miki ko wane ne attajiri Kulbus, sai dai na yi miki alkawari bayan mun samu matsugunni a can wata nahiyar daban zan bayyana miki wane Kulbus, ya cikar farin ciki na ki yi sani cewa sirrin da muka daɗe ni da mahaifiyarki muna ɓoye miki duka ya tattara ne akan attajiri Kulbus, ba domin ƙaddara ta sake haɗa mu da shi ba ko da sunan shi bana so kunnuwana su sake saurare har ajali ya riske ni",

Koda jin wannan batu daga bakin mahaifana sai ƙwalla ta zubo daga idanuna kuma na fahimci cewa haƙiƙa na aikata babban kuskure ga mahaifana na karɓar sadakar attajiri Kulbus,
Mahaifina ya sake duba na a karo na biyu ya ce "Sai ki yi hanzari mu isa izuwa gida kar duhun dare ya riske mu a hanya"
Koda jin hakan sai na riƙe sandar mahaifana muka cigaba da tafiya cikin hanzari suka fice daga kasuwar har muka nausa izuwa cikin daji,
Muna cikin tafiyar ne a cikin daji wanda mun saba huce ta cikin shi ba tare da wata fargaba ba,
Kaico! Haƙiƙa rashin sani ya fi dare duhu, kuma tabbas tashin hankali ba a sa masa rana,
Kwatsam! Bazato babu tsammani sai mu ka ji an ɓarke da wata irin mahaukaciyar dariya mai kama da haniniyar doki, jim! Kaɗan sai ga waɗansu zunzurutun samudawan dakaru na ratsowa daga cikin duhuwar bishiyun dajin,
Dakarun suna shirye cikin wata irin gagarumar shigar yaƙi mai matuƙar kwarjini da ban tsoro, suna ɗauke da miyagun makamai masu barazana ga rayuwar MUTUM DA ALJAN,
Komai dakewar zuciyar jarumi da rashin tsoron shi idan ya yi arba da Waɗannan dole ne ya ɗimauce,
Kafin mu yi wani yunƙuri dakarun sun yi mana ƙawanya suna muzurai tamkar za su ci babu, koda ganin hakan ban san lokacin da hawaye suka kwaranyo daga idanuna ba na riƙe hannun mahaifina.

Kwatsam! Bazato babu tsammani sai mu ka ji an bushe da wata mahaukaciyar dariya mai matuƙar ban tsoro, daga can sai sautin dariyar ya ɗauke, kawai sai dakarun dake ɓangaren yamma suka dare suka samar da wata 'yar siririyar hanya da mutum biyu za su iya jeruwa, kwatsam! Sai ga attajiri Kulbus ya ratso ta hanyar ya durfafo inda muke tsaye yana mai taka ƙafafuwanshi cikin ƙasaita fuskarshi a murtuke babu annuri, kuma a wannan lokaci yana shirye cikin gagarumar shigar yaƙi mai matuƙar kwarjini da ban tsoro, tun da nake a rayuwata ban taɓa ganin sadauki mai kwarjini tamkar attajiri Kulbus ba,
Ya yin da yazamana cewa tazarar dake tsakanin mu da shi ba ta huce taku goma ba sai kawai ya ja ta tsaya cak! Yana mai ƙura mana idanu ko ƙitawa ba ya yi,
Al'amarin da sanya tsoro ya sake kama ni ainun kenan jikina ya kama ƙyarma!,
Tsawon daƙiƙa talatin muna cikin wannan hali sai daga bisani ne attajiri Kulbus ya sake bushewa da dariya a karo na biyu sannan daga bisani ya murtuke fuska tamkar an aiko mashi da sakon mutuwa ya buɗi baki cikin kakkausar murya mai ban tsoro ya dubi abbana ya ce " Ya kai makaho Zafiyar ka yi sani cewa tsawon lokaci ina farautar ka a cikin wannan birni amma ban samu nasara ba sai a yau, ko ka manta cewa na faɗa maka indai kere na yawo zabo na yawo wata rana sai sun gamu",
Koda jin wannan batu daga bakin Kulbus sai mahaifana ya fusata ainun ya daka mashi tsawa ya ce " Ya kai babban maci amana kuma mayaudari ka yi sani cewa har abada ƙarshen maci amana mutuwar wulakanci, ina yi maka albishir da cewa yau zan hallaka ka".

Ko da jin wannan batu daga bakin abbana sai Kulbus ya bushe da dariya ya ce " Ya kai Zariyar ka fi kowa sanin cewa ko ba a gwada ba linzami ya fi ƙarfin bakin kaza, kar ka manta cewa a halin yanzu kai makaho ne idanuwanka ba sa gani, kuma tsufa ya fara kama ka ba ka da jarumtakar da za ka yin KARON BATTA da ni ba, sannan wannan 'ya taka ba ta da ƙarfin da za iya kare ka daga ka ba".

Kafin Kulbus ya gama rufe bakinshi na tari numfashin shi ina mai daka ma shi

tsawa na na buɗe baki da nufin na furta wani abu amma sai mahaifana ya dakatar da ni ta hanyar ɗaga mini hannu, kawai ya ɗaga sandarshi ya shammaci Kulbus ya make takobin sa ke hannunshi ya taƙarƙare ya gabza mashi wawan naushi a fuska da dukkan ƙarfin shi,
Saboda ƙarfin naushin sai da Kulbus ya yi taga-taga zai faɗi ƙasa amma sai ya turje ya shafa fuskarshi da hannunshi na hagu take ya ji jini na zuba a hancinshi,
Al'amarin da ya yi matuƙar bani mamaki kenan kuma ya ɗaure mini kai, domin a iya sani na mahaifana ko da wuƙar yankan tuffa bai iya riƙewa, amma ya ya aka yi ya samu wannan gagarumin ƙarfi haka? Amsar tambayar da na kasa bawa kaina kenan,
Shi kuwa attajiri Kulbus sai ya fusata ainun ya taƙarƙare ya kurma wawan ihu da ya firgita duk wata halitta dake dajin, yana gama rufe bakin shi sai dakarunshi suka zare makamansu suka yi ihu da kururuwa mai firgita DANDAZON MAYAƘA a FIKIN DAGA, suka ɗauki izuwa kan mahaifina,
Koda jin hakan sai mahaifana ya daka wawan tsalle tamkar an harba shi daga cikin baka ya sauka a daf da dakarun tamkar yakasance mai gani ba makaho ba, ya shammaci mutum huɗu a cikin su ya gabza masu wawan naushi a fuska a lokaci guda suka zube ƙasa magashiyan suna nishin wahala.
Lokacin da Jaruma Rusayyat ta zo dai-dai nan a labarin da take bawa su yaro Usaiba sai hawaye suka kwaranyo daga idanuwanta, sannan cigaba da cewa

BABI NA SHA SHIDA

Sa'adda na ga an kacame da azababban yaƙi tsakanin mahaifina da dakarun sai na ruga izuwa bayan wata bishiya na rakaɓe ina leƙen abin da ke wakana zuciyata cike da matuƙar mamakin jarumtaka irin ta abbana duk da kasancewar shi makaho,
Wani ɓangaren a zuciyata kuwa cike yake da tsoro akan abin da zai iya biyo baya idan attajiri Kulbus ya samu nasara akan abbana, wani tunani da ya faɗo mini a rai ya dungunzuma hankalina shi ne mahaifyata da baro a gida shin ko a wane hali take ciki,
Sa'adda na zo nan a tunanina sai hawaye suka kwaranyo mini,
Duk inda abbana ya sanya a gaba sai dai ka ga dakaru na zubewa ƙasa matattu tamkar ana karkaɗe busassu ganyeyya kin bishiya a lokacin hunturu, sassan jikkunan bil'adama suka dinga shawagi a sararin samaniya suna zubowa ƙasa, jini ya dinga kwanya, tsartuwa yana malala a ƙasa,
Nan da karafniyar ƙarafa da ihun MAZAJE  ta cika dodon kunne,
Wohoho! Haƙiƙa jarumtaka baiwa ce da zaɓi na Ubangiji dukiya ko mulki ba sa bayar da ita,
Komai hassadar mutum idan ya ga yadda makaho Zafiyar ke ragargazar dakarun dole ne ya jinjina mashi ya tabbatar da cewa ya shiga MURUCIN KAN DUTSE..,
"Sai da aka shafe tsawon sa'a ɗaya ana wannan Baƙin ARTABU babu sassauci,
Kasancewar masu iya magana na cewa SARKIN YAWA yafi SARKIN ƘARFI sai dakarun Kulbus suka fara galabaitar da mahaifana suka haɗa mashi jini da majina har ta kai cewa ya faɗi ƙasa magashiyan yana numfashi da ƙurar! Al'amarin da sanya ni zubar da hawayen baƙin ciki kenan,
Koda samun wannan gagarumar nasara sai attajiri Kulbus ya bushe da dariyar mugunta sannan daga bisani ya murtuke fuska tamkar an aiko mashi da sakon mutuwa ya zare wata sharɓeɓiyar

takobi a damtsenshi daga cikin kubenta ya taka da ƙafafuwanshi har izuwa inda mahaifana ke kwance ya sanya KAIFIN TAKOBI ya yi wa abbana yankan rago ya yi jifa da gawarshi gefe guda".
Lokacin da Jaruma Rusayyat ta zo dai-dai nan a labarin rayuwarta sai ta fashe da matsanancin kuka mai tsuma zuciya hawaye suna kwaranyo daga idanuwanta, al'amarin da ya sanya yaro Usaiba da yar uwarshi Hairat su ka fara zubar da hawayen saboda matuƙar tausayin ta, Tsawon daƙiƙa talatin suna cikin wannan hali sai daga bisani ne Rusayyat ta share hawayenta ta dube su a lokacin da idanuwanta suka kaɗa suka yi jajur ta ce " Ya ku 'ya'yana ku yi sani cewa wannan labari nawa da na ba ku ba a ɗauki kaso ɗaya bisa biyar ɗin shi ba, kuma wanda zan ba ku anan gaba ya fi shi ban tausayi da takaici".

Koda jin wannan batu daga bakin Rusayyat sai yaro Usaiba ya dube ta cikin alamun matuƙar damuwa ya ce " Ya ummina haƙiƙa attajiri Kulbus ya cika baƙin azzalumi marar tausayi, shin ta ya aka yi kika kuɓuta daga hannun shi sannan mene ne abin da ya faru da mahaifiyarki?, Koda jin waɗannan tambayoyi sai ƙwalla ta zubo wa Rusayyat ta dube shi ta ce " Ya ɗan abin alfahari na ka yi sani gaba ɗaya amsar tambayoyin da ka yi mini suna cikin ƙasashen labarina, yanzu za mu koma izuwa gida domin lokacin yin kalaci ya yi, zuwa gobe zan cigaba daga in da na tsaya". Koda gama faɗin hakan sai Rusayyat ta riƙe hannayen su suka tashi tsaye ta ɗora su a bisa wannan keken doki, ta hau ta zauna ta bisa dokin keken ta sakar ma shi linzami suka fara tafiya suna durfafar hanyar da zata sadasu da harabar gidan sarauta.

Wannan shi ne abin da ya faru tsakanin jaruma Rusayyat uwar gidan shugaban'yan fashin duniya sadauki fitinatul-Amir tare da su yaro Usaiba mai hatimin takobi.

Mu haɗu a Littafin TAFARKIN TSIRA 9 domin jin cigaban wannan ƙayataccen labari.
Daga mai ɗebe maku kewa lakabi da koyaushe.

MANSUR USMAN SUFI
Sarkin Marubutan Yaki
Wthapp Number
0813723771

TAFARKIN TSIRA 9
Littafin Yaƙi
Rubuta Labari
MANSUR USMAN SUFI
Sarkin Marubutan Yaƙi
Wthapp Number
08137237071

Littafan Marubucin

Kogon Annoba
Sarautar Mutuwa
Kangin Bauta
Jaruman Duniya
Takobin Ɗaukaka
Ƙarshen Zalunci
Fataucin Bayi
Sarkin Sadaukai
Goga Sha Fama
Tafarkin Tsira
Gasar Sarauta
Kundin Al'ajabi

BABI NA SHA BAKWAI

Lokacin da aka kacame da azababban yaƙi tsakanin sadauki ukaiza shugaban dakarun sarki Lamsarul-Azlam da ke farautar yaro mai hatimin takobi tare da dakaru dake tsaron ƙofar birnin Baitul-Ashmar, sai yaƙin ya zamto abin tsoro gami da tashin hankali, yawan dakarun ya zamo a banza domin ukaiza ya wanzu yana aika rayukan su izuwa barzahu KAIFIN TAKOBInsa ya dinga ratsa sassan jikkunan su JINI DA ƘASA suna cakuɗuwa da juna,
Kaifin shudewar daƙiƙa hamsin ukaiza ya hallaka fiye da rabin dakarun, al'amarin da ya razana sauran kenan domin tun da suke gadin wannan ƙofa ba a samu GWARZON MAYAKI da ya samu nasara akan su na shin  wane ne wannan sadauki? Amsar tambayar da suka kasa bawa kansu kenan,
Ana cikin wannan ARTABU ne wani tunani ya faɗo wa ukaiza tunanin kuwa shi ne, idan har ka bari aka ɗauki wani lokaci ba tare da ka yi nasara ba to dakarun dake cikin gari za su samu rahoton abin da ke faruwa domin haka za a tsaurara matakan tsaro,
Sa'adda Ukaiza ya zo nan a tunanin shi sai kawai ya dinga amfani da hikima ya na kashe fitilun dake wajen , yayin da ya fahimci cewa wajen ya yi dubu dunɗum! Sai kawai ya shammaci dakarun ya kunna kai izuwa cikin birnin, ya bar dakarun suna ta ƙoƙarin kunna fitilun, kai tsaye gidanshi ya nuna domin ya ga wane hali iyalinshi ke ciki,
Lokacin da isa sai ya tarar ƙofar gidan a buɗe kuma ko wane waje a ciki haskake yake da fitilar ice, al'amarin da ya yi matuƙar ba shi mamaki kenan, kuma zuciyarshi ta buga da ƙarfi, amma sai ya kunna kai izuwa ciki yana sanɗa hannunshi dafe da kuben takobinshi domin shirin kar ta kwana, ya yin da ya yi kamar taku shida a zauren gidan sai kawai ya ji an gabza ma shi wani wawan naushi a ƙeyarshi saboda matuƙar ƙarfin naushin sai da ya yi katan-tanwa sai uku sai ya

faɗi ƙasa tim! A matuƙar galabaice yana mai kurma ihu, kafin ya yi wani yunƙuri waɗansu irin samudawan  dakaru ma'abota jajayen tufafi sun ɗaure shi tamau da wata irin murtukekiyar igiya sannan ɗaya daga cikin su ya ɗauke shi ya ɗora shi a kafaɗarshi ya nufi ƙofar fita daga gidan, sauran dakarun mutum shida suka yi koyi da shi, suna fita kai tsaye suka durfafi wata hanya da zata sadasu da kurkukun birnin suna tafiya cikin hanzari.

Wannan shi ne abin da ya wakana tsakanin sadauki ukaiza da dakarun sarki Lamsarul-Azlam.

Al'amarin boka kaddad kuwa tun sa'adda ya tura aljani Lattul-kifas domin farauto mishi yaro mai hatimin takobi sai ya shafe tsawon kwanaki biyu bai ji ɗuriyar shi ba, yayin da ya fahimci cewa wankin hula zai kai shi dare sai kawai ya yanke shawarar ya gudanar da bincike bisa halarar tsafin shi domin gano abin da ke wakana,

Sa'adda ya gudanar da bincike nan take ya ga dukkan abin da wakana tsakanin Lattul-kifas da dakarun dake gadin gidan sarkin 'yan fashin duniya sadauki fitinatul-Amir, koda ganin hakan sai ya taƙarƙare ya kurma wawan ihu, sautin ihun ya amsa kuwwa har izuwa cikin dajin ya tashi ha hankulan tsuntsaye dake kan bishiyu suka bazama wajen canja sheƙunansu,

Tsawon daƙiƙa ashirin yana cikin wannan hali sai daga bisani ne ya murtuke fuska an aiko mishi da sakon mutuwa,

Sannan ya sake baje alƙalumman sihirin shi ya cigaba da gudanar da bincike, yana cikin wannan hali ne kuma sai ya taƙarƙare ya bushe da dariyar farin ciki,

Ba wani abu ne ya sanya shi wannan dariya ba sai domin ya gano cewa har abada ba zai taɓa cimma burin shi na shan jinin yaro mai hatimin takobi ba kuma har ya kawar da Jaruma Rusayyat da mai gidanta ba face ya mallaki wata hula da ake yiwa laƙabi da Lauhul-Sihir,

Hular Lauhul-Sihir ta kasance mallakin sarkin bokayen aljanun duniya wanda a ƘARNI UKU bayan yaƙin duniya na farko ba a samu GWARZON MAYAKI tamkar shi ba,

Binciken masana da masu hasashe ya tabbatar da cewa boka ƙaddamul-Barzahu yana iya yaƙar gari guda shi ƙadai ya cinye shi da yaƙi b zai bar koda ƙiyashin birnin a raye ba,

Kuma an ce ya shafe tsawon shekaru ɗari bakwai yana sana'anta hular Lauhul-Sihir bayan ya kammala ne ya shiga yaƙar sarakunan duniya yana mayar da su izuwa ƙarƙashin ikon shi, wata ƙasa ce ta ma'abota addinin musulunci kawai ta zamo mishi cikas wajen cimma burin shi na BAUTAR SARAKAI na duniya, bisa wannan dalili yasanya masana ke yi masa laƙabi TARKON SARAKAI,

Daga cikin amfanin da hular Lauhul-Sihir shi ne duk mahalukin da ya mallake ta zai mulki dukkan sarakunan duniya,

Tana ɗauke da sirrkan tsafi guda miliyan biyu da babu wanda zai same su face wanda ya mallaki hular,

Duk wanda ke sanye da hular zai iya shafe tsawon sa'o'i yana ARTABU ba tare da ya ci ko ya sha ba,

Babu wani makami da zai yi tasiri akan shi, duk tsawon shekarun da mutum ya shafe yana jinya inda aka sanya mishi ita nan take zai warke sumul tamkar bai taɓa jinya ba,

Sirri na ƙarshe shi ne mutum na iya sanya hular izuwa kowa ne nau'in makami kuma ya aikata zuwa inda yake so ta aiwatar da dukkan abin da ya nufa,

A halin yanzu hular Lauhul-Sihir tana ajiye a wani kogon dutse mafi haɗari a duniya, kafin mutum ya isa inda yake sai ya ƙetare waɗansu miyagun dazuka guda sha biyu,

Babu wani mahaluki da doran ƙasa da zai iya shiga kogon face ya mallaki wani ALLON SIHIRI, Allon yana ajiye a cikin wani masifaffen kada dake zaune a ƙarƙashin tekun Baharul-Saljir, kadan ya haɗiye Allon ne a lokacin da waɗansu manyan matsafan duniya suka fafata yaƙi a saman tekun domin ɗayan su ya mallaki ALLON SIHIRIn,
Wannan shi ne abin da yasanya boka kaddad ya yi wannan dariyar farin ciki,
Tun daga wannan rana kaddad ya fara shirye-shiryen tafiya domin mallakar hular Lauhul-Sihir.
Wannan shi ne abin da faru da boka kaddad bayan ya tura hadimin aljanin shi domin farauto mishi yaro mai hatimin takobi.

BABI NA GOMA SHA TAKWAS

Al'amarin shugaban 'yan fashin duniya sadauki fitinatul-Amir kuwa, tun sa'adda uwar gidanshi Rusayyat ta shayar da shi hodar banju domin ta samu nasarar tseratar da rayuwar yaro Usaiba mai hatimin takobi. Sai ya shafe tsawon kwana ɗaya a cikin wannan hali sannan ya farka ta hanyar buɗewa idanuwanshi ya yi miƙa gami da hamma, kuma ya ji kanshi na juya mishi,
Kawai sai ya ƙwalla wa wata kuyanga kira,bayan ta bayyana gare shi ta zube ƙasa ta kwashi gaisuwa sai ya dube ta ya ce "Ya ke mushlaira shin har tsawon wane lokaci na ɗauka ina barci kuwa?
Koda jin wannan tambaya sai Mushlaira sai ta buɗi baki cikin ladabi ta ce "Ya shugabana ai yau tsawon kwana ɗaya kenan ka shafe kana barci"
Sa'adda fitinatul-Amir ya ji wannan batu sai ya cika da matuƙar mamaki da al'ajabi, har buɗe baki da nufin yace wani abu sai ya ji alamun ɓuɗe ƙofar turakar don haka sai mayar da duban shi izuwa ga wajen domin ya ga wane ne ke tafe.
Aikuwa sai ya yi arba da uwar gidanshi Rusayyat ta caɓa ado mai ƙayatarwa fuskarta cike da annuri,
Koda Mushlaira ta yi ga cewa gimbiya ta shigo sai ta miƙe tsaye zumbur! Ta durfafi ƙofar fita daga turakar,
Sannu a hankali Rusayyat tana takawa da ƙafafuwanta har ta iso inda mai gidanta yake ta zauna a daf da shi har suna jin numfashin juna,
Cikin tattausan murmushi mai ɗimauta zuciya Rusayyat ta ce "Barka da wannan lokaci ya JARUMIN JARUMAI farin cikin zuciyata", fitinatul-Amir ya mai da mata da martanin murmushin, wanda ya fi kama da yaƙe sannan yayi gyaran murya ya ce "Ya uwar'ya'yana wai shin tsawon wane lokaci na ɗauka ina wannan barci ne?
Da jin wannan tambaya sai Rusayyat ta ce "Ya abin ƙaunata ai baka huce tsawon sa'a ɗaya ba, ko ka manta ne cewa ɗazun nan ba jimawa muka yi kalaci yanzu kuma da farka ai lokacin fita faɗa ne",
Koda jin amsar wannan tambaya sai tunanin fitinatul-Amir ya rikice yace a cikin ranshi, shin tsakanin matata da kuyanga Mushlaira wane ne ya raina mini hankali? Tabbas duk wanda na samu da laifin hakan sai na yanke mishi hukunci mai tsanani",
Koda gama tunanin hakan sai ya miƙe tsaye ya nufi kewaye, jim! Kaɗan ya fito bayan ya tsaftace fuskarshi ya riƙe hannun Rusayyat suka durfafi ƙofar turakar, suna fita waɗansu zaratan dakaru masu jajayen sulke ɗauke da miyagun makamai suka mara masu baya,

Duk wajen da suka durfafa a cikin gidan sarautar sai ka ga dakaru, kuyangi da hadimai na zubewa ƙasa suna kwasar gaisuwa cikin girmamawa, yayin da aka iso daf da turakar Rusayyat sai suka yi bankwana fitinatul-Amir da sauran dakarun kuma sai suka ci-gaba da tafiya,
Tafiyar daƙiƙa arba'in kacal! Suka yi aka iso fadar birnin,
Ita dai fadar ta kasance ƙasaitacciya da aka yi mata ado da nau'ikan kayan ƙawa da alatun more rayuwar duniya, gaba ganin fadar an yi shi ne da zallar jauhari da zubar-daju,
Masana da masu hasashe sun tabbatar da cewa babu wata faɗa da ta kai ta ƙawatuwa, waɗansu daga cikin masana na kiran fadar da suna ALJANNAR DUNIYA.

Kai tsaye fitinatul-Amir ya nufi inda karagar mulki take ya taka matattakalar fadar, a lokacin da gaba ɗaya jama'ar fadar suka miƙe tsaye domin girmamawa a gare shi,
Bayan Fitinatul-Amir ya hakimce bisa karagar mulki sai suka dinga tashi daga wajen zamansu suna zuwa gare shi suna kwasar gaisuwa, talakawa ne suka fara tasu gaisuwar sannan attajirai, sai 'yan majalisar sarki, su dai 'yan majalisar sun kasance GWARAZAN JARUMAI da Fitinatul-Amir ke amfani da su domin kai farmaki zuwa wata ƙasa, don FATAUCIN BAYI da ganimar dukiya, mutum shida daga cikin 'yan majalisar sun kasance GWARAZAN SARAKAI saboda matuƙar tsoron Fitinatul-Amir ya sanya suka haƙura suka bar sarautar suka koma KANGIN BAUTA a ƙarƙashin shi. Shiru ne ya wanzu a fadar na tsawon lokaci tamkar an yi ruwa an ɗauke, sai daga bisani ne wani garjejen ƙato mai ƙirar samudawan farko daga cikin 'yan majalisar ya buɗi baki cikin ladabi da ƙasƙantar da kai ya buɗi baki ya ce "Ya shugabana yau tsawon kwanaki uku kenan Ayarin sarakuna guda ashirin suna so su gana da kai domin su bayar da harajin su kamar yadda suka saba"
Koda jin wannan batu daga bakin ɗan majalissar sai Fitinatul-Amir ya sake cika da matuƙar mamaki ya dube shi ya ce "Ya kai Haibatu shin yau har na kai tsawon kwanaki uku ban fito fada ba?,
Haibatu ya ce "Kwarai kuwa ya shugabana"
Shin yanzu wane ne ya raina mini hankali uwar gidana, kuyanga Mushlaira ko kuwa Haibatu?,
Amsar tambayar da Fitinatul-Amir ya kasa bawa kanshi kenan, sannan ya sake bude baki a a karo na biyu yana duban Haibatu ya ce " Ka sanar da sarakunan cewa ba zan samu damar ganawa da su a yau ba dai zuwa gobe",
Daga wannan batu ne ya yi shiru aka cigaba da gudanar da sha'anin mulki kamar yadda aka saba.

Mu haɗu a littafi na 10 domin jin cigaban wannan ƙayataccen labari.
Daga mai ɗebe maku kewa a kullum da koyaushe.

Mansur Usman Sufi
Sarkin Marubutan Yaki
Wthapp Number
08137237071

TAFARKIN TSIRA 3
Littafin Yaki
Rubuta Labari
Mansur Usman Sufi
Sarkin Marubutan Yaƙi

Littafan Marubucin

Kogon Annoba
Sarautar Mutuwa
Kangin Bauta
Jaruman Duniya
Takobin Ɗaukaka
Ƙarshen Zalunci
Fataucin Bayi
Sarkin Sadaukai
Goga Sha Fama
Tafarkin Tsira
Gasar Sarauta
Kundin Al'ajabi
Turbar Ajali
Farautar Mazaje

Littafin kudi ne ₦300
Za'a biya kudin ta wannan account
0084279025
Usman Umar Mansur
Accces bank
Sai a tura shaidar biya ta wannan Number
08137237071

BABI NA SHA TARA

A can birnin Zainul-Ansar kuwa sai da aka shafe tsawon kwanaki uku ana bawa sarki Nu'umanu kulawa sosai ya warke sumul. A iya tsawon waɗannan kwanaki wannan hadimi mai ɗauke da siffa irin ta waziri Yazid shi ne ke lura da dukkanin wani sha'ani na masarauta, kuma duk bayan wani lokaci sai ya ziyarci turakar sarki ya ga a wane hali yake ciki a sirrance batare da wani ya gane shi ba.
A ɓangaren sarkin yaƙi lauzar kuwa shi ma ya gudanar da aiyukan da waziri ya umarce shi batare da wata matsala ba.
A safiyar wata rana ne sarki Nu'umanu ya aike wa da dukkan 'yan majalisar shi da saƙon zaman majalisar zartarwa,
Sa'adda sarki ya ga cewa kowa ya hallara a fadar kuwa an yi shiru sai ya yayi gyaran murya ya ce "Godiya ta tabbata ga Allah maɗaukakin Sarki bisa iko da ya bamu na halartar wannan taro mai albarka, tsira da amincin shi su ƙara tabbata ga Manzon tsira, bayan haka ya ku dattawam wannan masarauta tamu mai albarka bakomai ne ya sanya na tara ku a anan ba sai domin tattaunawa akan abin da ya faru a wannan birni namu na harin bazato daga maƙiya, shin yanzu wa ake tunanin ya kawo mana farmakin, sannan wane mataki ya dace mu ɗauka domin kare afuwar hakan?
Sa'adda sarki ya zo dai-dai nan a jawabin shi sai fadar ta yi tsit babu wanda yace ƙala tsawon daƙiƙa talatin sai daga bisani ne wani kyakkyawan saurayi ma'abocin kwariji wanda shi ne magatakarda ya yi gyaran murya ya ce "Ya 'yan uwana dattawam wannan masarauta mai albarka ku yi sani cewa abin da bincike ya tabbatar mini a harin bazato da aka kawo mana tabbas anyi amfani da shiri,
Hujja ta farko shi ne masu ba su ƙyale wata alama da zamu iya bincike akai ba tun daga gawarwakin dakarunsu, takobi ko tufafi,
Hujja ta biyu lokacin da na hallaka wani ɗan MAMAYAR BAZATO naga hatimin wata masarauta a jikin sulkenshi sai dai ban tsaya na lura da na wace masarauta ba ne,
Waɗannan hujjoji da na zayyana za su tabbatar mana da cewa waɗanda suka kawo farmakin sun kasance ma'abota bautar wanin Allah,
Ta wata fuskar zan iya cewa da alamu akwai wani munafuki a cikinmu da labartawa sarki Rakibu tattaunawar zaman da mu kayi a makon da ya gabata".
Lokacin da magatakarda ya zo dai-dai nan a zancen shi sai kowa ya sha jinin jikinshi kuma ya zurfafa izuwa kogin tunani, wannan hadimi mai ɗauke da siffa irin ta waziri da sarkin yaƙi Lauzar kuwa sai suka ji hantar cikinshi ta kaɗa da ƙarfi suka dinga yiwa junansu inkiya ta wutsiyar idanu batare da wani ya lura da su ba.
Shugaban Baitul-Mali yayi gyaran murya sannan ya ce "Hakiƙa abin da magatakarda ya faɗi zai iya zamowa gaskiya, domin kuwa idan bamu manta ba Ubangiji ya faɗa a cikin littafinshi mai tsarki cewa kar mu riƙe kafirai a matsayin masu jiɓintar lamuran mu, domin su na yin umarni ne da hanyar shaiɗan...
Kafin ya gama rufe bakinshi magatakarda ya tari numfashi yana mai cewa "Ban katse ka ba ta kai ma'aji amma kafi kowa sanin cewa ba ma da wata hujja da za mu iya tuhumar sarki Rakibu bisa zargin da muke yi mishi, sannan kar ka manta cewa shi ne sarki da yafi kowa kyautata zumunta da zaman lafiya tsakanin mu da shi a kaf masarautun dake wannan nahiya tamu.
Shawarar da zan bamu anan ita ce tsaurara matakan tsaro domin a fahimta ta sakacin dakaru masu tsaron ƙofa shi ne ya haifar da MAMAYAR BAZATO, wannan ita ce shawarata Allah ya taimake ka".

Lokacin da waziri Yazid yazo nan a zancen shi sai zauren majalissar ya sake yin shiru a karo na uku tsawon daƙiƙa talatin ana cikin wannan hali babu wanda ya ce uffan, koda ganin hakan sai sarki Nu'umanu ya miƙe daga kan karagarshi yayi gyaran murya a karo na biyu sannan ya buɗi baki ya ce "Ya ku 'yan majalissata ku yi sani cewa tun da bamu tsayar da magana ɗaya ba, ya zama wajibi mu sake dogon nazari domin nemo bakin zaren, amma kafin wannan lokaci ba shiru za mu yi ba dole ne mu ƙara ƙarfin mayaƙanmu dodon tsaurara matakan tsaro, sannan akwai buƙatar mu yawaita idanuwansu a cikin al'umma domin samun bayanan sirri, da wannan batu nake yi maku fatan alheri sai Ubangiji maɗaukakin SARKI ya sake haɗa fusakun mu".

Koda gama faɗin hakan sai ya sauko ƙasa yana takawa da ƙafafuwanshi ya durfafi wata ƙofa ta musamman dakaru ma'abota fararen tufafi suka mara mishi baya har sai da suka ƙule izuwa cikin ƙofar, sannan taron ya watse kowa ya kama gabanshi.
Wannan shi ne abin da ya wakana a can birnin Zainul-Ansar bayan harin sumane daga dakarun haɗin gwiwa.

Dukkan abin da ya wakana a wannan tattaunawa da sarki Nu'umanu ya yi da 'yan majalisar shi, sarki Rakibu da waziri Yazid sun gani a cikin madubin tsafin waziri a lokacin da suke zaune a wani lambun shaƙatawa, koda ganin wannan al'amari sai hankalin sarki Rakibu ya DUGUNZUMA ainun ya dubi waziri cikin matuƙar damuwa ya ce "Ya abokina tabbas a yanzu muna halin TSAKA MAI WUYA idan har sarki Nu'umanu ya gano cewa mu ne muka kai mishi MAMAYAR BAZATO".
Koda jin wannan batu sai waziri ya yi shiru yana mai juya al'amarin a cikin ranshi, daga bisani ya tattare hankalin shi waje guda ya dubi Rakibu ya ce "Ya kai babban aminina Kabul sani cewa koda ace sarki Nu'umanu ya gano shirin mu wannan ba zai sanya mu janye aniyar mu ta kawar da shi daga doran ƙasa ba, babban abin da nake ganin zai iya haifar mana da matsala shi ne ma'aji Kulairu,
Na fi kowa sanin wane shi domin mutum mai naci da juriya akan dukkan abin da ya sanya a gaba sai ya cimma nasara, ya zama wajibi a gare mu mu gana da shi a wannan dare, sannan za mu nufi birnin Zainul-Ansar ta dakarun yaƙin mu amma ba zamu kai farmaki ba sai lokacin da alfijir ya keto za a gudanar da sallar asuba, ina mai tabbatar maka da cewa zamu samu gagarumar nasara a wannan karon".
Lokacin da waziri ya zo dai-dai nan a zancen shi sai sarki Rakibu ya cika da matuƙar farin ciki maral-musaltuwa.

Wannan shi ne abin da ya wakana tsakanin waziri Yazid na gaskiya da sarki Rakibu bayan sun ga dukkan tattaunawar sarki Nu'umanu da 'yan majalisar shi.

Mu haɗu a Littafin TAFARKIN TSIRA 11 domin jin cigaban wannan ƙayataccen labari.
Daga mai ɗebe maku kewa a kullum da koyaushe.
Mansur Usman Sufi
Sarkin Marubutan Yaƙi

08137237071
TAFARKIN TSIRA 11
Rubuta Labari
MANSUR USMAN SUFI
Sarkin Marubutan Yaƙi
08137237071

ELEGANT ONLINE WRITER'S

Littafan Marubucin

Kogon Annoba
Sarautar Mutuwa
Kangin Bauta
Jaruman Duniya
Takobin Ɗaukaka
Ƙarshen Zalunci
Fataucin Bayi
Sarkin Sadaukai
Goga Sha Fama
Tafarkin Tsira
Gasar Sarauta
Kundin Al'ajabi

Koda jin wannan batu daga bakin sarki Rayyan sai jama'a suka samu ƙarfin gwiwa dukkan fargaba,
Lokacin da yazamana tarar da ke tsakanin rundunonin biyu bai huce taku talatin ba sai kowanne ya ja ya tsaya aka yi kallon-kallo na tsawon daƙiƙa hamsin daga bisani sai sarki Lamsarul-Azlam ya ƙatse shirun da wanzu ta hanyar bushewa da dariyar mugunta sannan daga bisani ya murtuke fuska tamkar an aiko mashi da SAƘON MUTUWA ya buɗi baki cikin kakkausar murya mai kama da kukan jaki ya ce "Ya kai tsohon abokin gaba kuma sarki mai taurin kai wajen biyayya a gare mu ka yi sani cewa yau ita ce rana ta ƙarshe da zan shafe tarihin ka daga doron ƙasa, domin kai ganau ne ba jiyau ba kuma ko ba a gwada ba linzami ya fi ƙarfin bakin kaza, kuma wutsiyar raƙumi ta yi nesa da ƙasa, ba za ka iya ja dani domin har abada ruwa ba sa'an kwando ba ne..."
Kafin ya gama rufe bakinshi sarki Rayyan ya tari numfashin shi yana mai daka mashi tsawa ya dube shi ya ce "Karya kake ya tsahon mafi amana ka yi sani cewa komai matuƙar yawan rundunarka bazai firgita ni ba domin Ubangiji shine mai bayar da nasara, sannan har abada ƘARYA DA GASKIYA ba sa haɗuwa waje guda guda face gaskiya ta yi RINJAYE.

Koda jin wannan batu daga bakin sarki Rayyan sai Lamsarul-Azlam ya fusata ainun gashin jikin shi ya mimmiƙe kawai sai ya zare wata sharɓeɓiyar Adda mai matuƙar KAIFI DA TSINI ya sakarwa dokinshi linzami yana ihu da kururuwa mai firgitarwa ya durfafi sarki Rayyan, koda ganin hakan sai shi ma ya yi koyi da shi ta hanyar zare takobinshi ya yi ɗauki kanshi yana ƙwala kabbara, lokacin da suka zo daf da juna sai Lamsarul-Azlam ya kai mishi wawan sara a kafaɗa, cikin matuƙar zafin nama Rayyan ya sanya garkuwarshi ya kare harin sannan suka ruguntsume da azababban yaƙi mai matuƙar kwarjini da ban tsoro, suka yi KARON BATTA irin na GWARAZANA JIYA.

Lokacin ɓangarorin biyu suka ga cewa jagororin su sun ruguntsume da artabu sai suka ɗaga makaman su suka yi ɗauki kan juna kafurai na ihu da kururuwar banza, musulmi na kabbara lokacin da aka haɗu sai aka rincaɓe da BAƘIN ARTABU ƙarar karafniyar ƙarafa haɗe ihu da kururuwar mazaje ta cika dodon kunne.

Haƙiƙa yaƙi shine matattarar dukkan wata musiba da zata samu ɗan Adam a doron ƙasa, domin yaƙi shine ke raba uwa da ɗan ta, asarar dukiya da rayuwa ma baki ɗaya.

Kaico! Inda ace mutum yana tsaye a wannan waje lokacin da kofatun dawakai ke kartar ƙasa suna tayar da ƙura, Hargowar aljanu da bil'adama JINI DA KASA suka cakuɗe waje guda MUTUWAR MAZAJE ta fara gudana dole ya ɗimauce.
Wannan shi ne abin da ya faru a lokacin da sarki Lamsarul-Azlam da rundunarshi suka isa izuwa birnin MADINATUL-AFNAN.

## BABI NA ASHIRIN DA ƊAYA

Al'amarin shugaban'yan fashin duniya sadauki fitinatul-Amir kuwa lokacin da ya baro fada cikin matuƙar fushi bisa ga amsar tambayar da ɗan majalisa Haibatu ya faɗa mashi akan cewa yau tsawon kwanaki uku bai fito zaman fada ba, sai ya huce kai tsaye izuwa turakar su yaro Usaiba domin ya tabbatar da zargin da zuciyarshi take yi, lokacin da ya isa masu gadi suka buɗe mashi ƙofar turakar ya kunna kai izuwa ciki sai ya tarar da suna sharar barci a bisa kan gado, domin haka sai ya isa bakin gadon cikin hanzari ya sanya hannunshi ya ɗage jigar dake jikin Usaiba ya duba gadon bayanshi, aikuwa sai ya ga wayam babu zanen hatimin takobin SAIFUL-ZAYYAD, domin haka sai ya juya ya fice daga turakar zuciyarshi cike da matuƙar mamaki ainun,
Abu na farko da ya bashi mamaki shine shin mene ne yasanya zuciyarshi take bugawa da ƙarfi a duk lokacin da ya yi arba da yaro Usaiba,
Anya kuwa uwargidanka Rusayyat ba zata ci Amanar ka ba ta tseratar da rayuwar yaron.
Wata zuciyar kuma ta ce da shi ta ya ya kake tsammanin zata ci amanar ka bayan cewa za ta fi kowa burin ace ta samu haihuwa domin samun magaji. Lokacin da yazo dai dai nan a tunanin shi sai hankalin shi ya kwanta ya ji ya gamsu cewa yaro Usaiba ba shine mai hatimin takobi ba.
Wannan shi ne abin da ya faru da sarkin 'yan fashin duniya sadauki fitinatul-Amir.

Fadar ta ƙawatu ainun da nau'ikan kayan ƙawa gami da alatun jin daɗin rayuwar duniya har da abin da idanu ba su taɓa gani ba, duk ƙasaitar BASARAKE ko attajiri idan ya tsinci kanshi a wannan fada dole ya tabbatarwa kanshi cewa GABA DA GABANTA aljani ya taka wuta, a wannan lokaci fadar ta cika maƙil babu masaka tsinke duk inda mutum ya kalla kawunan bil'adama ne rututu babu masaka tsinke, a kowacce kusurwa a dakarun tsaro ne shirye cikin

gagarumar shigar yaƙi mai matuƙar kwarjini da ban tsoro suna ta kai komo domin tabbatar da cikekken tsaro.

Bisa wani zagayayyen tudu mai matattakala bakwai a ƙasan shi anan aka ajiye wata ƙasaitacciyar karagar mulki da aka sana'anta ta da ƙarfen zubar daju aka yi mata feshi da koren lu'ulu'u, wani shirgegen mutum ne tamkar giwa, ƙasumba da sajen shi baƙaƙe siɗik! Sune suka tona asirin kyawun surarshi, kuma suturun dake jikinshi suka dace da shi, kallo ɗaya za ka yi mashi ka fahimci cewa ya cika GWARZON MAYAƘI mai ƙarfi na Allah ya isa, a wannan lokaci fadar ta yi tsit tamkar mutuwa ta kawo ziyara, kwatsam! Bazato babu tsammani sai aka ga wani mutum ya bayyana tsulum! A tsakiyar fadar tamkar an aiko shi daga sama, mutumin yakasance gajere baki wuluk! Fuskarshi mummuna ce tamkar bai taɓa dariya ba, jikinshi cike yake da gashi buzu-buzu da layi, da guraye na sihiri babu kyawun gani tamkar wani tsohon mahaukaci, babu wani tufafi a jikinshi face bante na fatar damisa da ya suturce al'amuran shi, a hannunshi na hagu yana dogare da wata SANDAR TSAFI, kaico! Haƙiƙa babu wani mahaluki a doron ƙasa da zai yi arba da wannan mutum ba face ya firgice, ba wani ba ne face boka kaddad.
Sannu a hankali kaddad ya yi tattaki da ƙafafuwanshi yana mai dogara sandarshi ya durfafi inda karagar mulki take, lokacin da ya rage saura kamar taku goma ya isa sai ya zube ƙasa ya kwashi gaisuwa cikin girmamawa,
Cikin annuri fuska mutum dake zaune bisa karagar ya ƙarɓi gaisuwar ta hanyar gyaɗa kai sannan ya buɗe baki cikin kakkausar murya mai kama da saukar aradu ya ce "Lale marhabun da Dodon bakoye hadari malafar duniya, lafiya na gan ka a wannan lokaci da baka saba zuwa ba ?
Koda jin wannan tambaya sai boka kaddad ya buɗe baki a karo na farko cikin murya mai kama da haushin kare ya ce "Ya shugabana ka ji sani cewa bakomai na ya kawo ni gare ka sai domin na sanar da kai wani abin farin ciki, bincike da na gudanar bisa halarar tsafi na ya bayyana mini maganin da zai warkar da gimbiya da cutar makanta da take damun ta, shi ne wani ALLON TSAFI, dake ajiye a ƙarƙashin tekun Baharul-Saljir a cikin wani masifaffen kada,
Ya kai Hulaifu ka yi sani cewa a halin yanzu a duniya babu wata dabba dake rayuwa a cikin teku da ta kai kadan ƙarfin damtse da na sihiri,
Za a warkar da gimbiya ne idan aka karanta ɗalasiman tsafin dake jikin Allon sannan a shafa mata a fuska take idanuwanta za su buɗe garau!"

Koda jin wannan jawabi daga bakin boka kaddad sai sarki Hulaifu ya cika da matuƙar farin ciki maral-musaltuwa fuskarshi ta faɗa da murmushi ya dube shi ya ce "Ya masanin ilimin tsafi tsawon lokaci za mu ɗauka kafin tafiya nemo wannan ALLON TSAFI?
Boka kaddad ya bushe da dariyar mugunta sannan ya ce "Ai a gobe za mu yi wannan tafiya domin masu iya magana na cewa da zafi-zafi akan daki ƙarfe, kuma a bari ya huce shi ke kawo rabon wani, sai dai dole ne tafiyar sai an tafi da gimbiya domin kuwa Allon yana da wani sharaɗi idan har aka fito da shi daga gadan idan har ya huce tsawon sa'a ɗaya ba ayi amfani da shi ba zai lalace kaga kenan an sha wahalar banza".

Koda jin wannan batu daga bakin boka kaddad sai sarki Hulaifu ya cika da matuƙar farin maral-musaltuwa, take kaddad ya sake ɓace ɓat tamkar bai taɓa wanzuwa ba, sarki ya tashi daga faɗa ya shiga izuwa cikin gidan sarauta, kowa ya watse ya kama gaban shi.

Mu haɗu a TAFARKIN TSIRA 12 Domin jin cigaban wannan ƙayataccen labari.
 Daga mai ɗebe maku kewa a kullum da koyaushe.

MANSUR USMAN SUFI
Sarkin Marubutan Yaƙi
Wthapp Number
08137237071

TAFARKIN TSIRA 12
Rubuta Labari
MANSUR USMAN SUFI
Sarkin Marubutan Yaƙi
Wthapp Number
08137237071

Littafan Marubucin

Kogon Annoba
Sarautar Mutuwa
Kangin Bauta
Jaruman Duniya
Takobin Ɗaukaka
Ƙarshen Zalunci
Fataucin Bayi
Sarkin Sadaukai
Goga Sha Fama
Tafarkin Tsira
Ƙarya Da Gaskiya
Gasar Sarauta

BABI NA ASHIRIN DA BIYU

Kashe gari tunda duku-dukun safiya bayan shugaban 'yan fashin duniya sadauki Fitinatul-Amir ya yi kalaci ya caɓa ado sai nufi fada domin ganawa da sarakunan da zasu gabatar da haraji. Bayan kowa ya hallara sarki ya hakimce bisa karaga 'yan majalisa sun kammala mika gaisuwa,

Lokacin da sarakuna birane ashirin da uku suka gurfana a gaban sadauki Fitinatul-Amir sai sarki na farko da ake kira da suna Madsur ibn Zauhil ya faɗi ya yi gaisuwa sannan ya buɗi baki cikin ladabi kanshi a sunkuiye ya ce "Ya sarkin sarakuna, GOBARAR DAJI mai share abokan gaba, KAIFIN TAKOBI mai raba tsakanin masoya, kai ne SARKIN SADAUKAI GOGA SHA FAMA dake saukar da ANNOBA ƊARI, gani tafe da ɗan abin da bai taka kara ya karya ba ina roƙon a ƙarɓa domin na kai ba".

Koda jin wannan batu daga bakin sarki Madsur sai Fitinatul-Amir ya bushe da dariyar farin ciki maral-musaltuwa bisa kirarin da ya yi mashi, sannan daga bisani ya murtuke fuska tamkar an aiko mashi da SAƘON MUTUWA ya dube shi cikin taƙama da BAKAR IZZA ya ce "Yakai Madsur haƙiƙa dukkan abin da ka faɗa gaskiya ne saboda haka dukkan abin da ka kawo an karɓa tafi abin ka".

Cikin matuƙar farin ciki dakarun sarki Madsur suka gabatar da dinaren harajin dake cikin waɗansu akwatu na baƙin ƙarfe, sannan sarki ya ja ya koma ya gefe guda

Sarki na biyu mai suna Ashrum dake mulkin birnin Darul-Zabub ya faɗi ya kwashi gaisuwa ya buɗi baki ya yi gyaran murya kanshi a sunkuiye ya ce "Ya shugabana gani tafe da dukkan abin da aka buƙata, ina fatan dukiyata za ta zamo fansa gare ni da al'ummata"

Koda jin wannan batu daga bakin sarki Ashrum sai Fitinatul-Amir ya fusata ainun ya daka mashi tsawa wacce ta sanya hantar cikinshi Ashrum ta kaɗa jikkunansu suka kama ƙyarma, cikin matuƙar fushi Fitinatul-Amir ya dube shi "Ya kai Ashrum shin wace dukiya gare ka da zata fansar da Jinin al'ummarka? Haƙiƙa ka yi Furuci mafi muni a gare mu da wajibi ne sai mun ganar da kai kuskuren ka,

Koda jin wannan batu daga bakin Fitinatul-Amir sai sarki Ashrum ya faɗi ƙasa yana neman gafara yana mai cewa "Ina tuba ya shugabana tabbas na yi kuskure....,

Kafin ya gama rufe bakinshi Fitinatul-Amir ya dako wawan tsalle daga kan karagarshi tamkar an harbi shi daga cikin baka ya shammaci Ashrum ya kirɓa mashi wawan naushi a wuya, saboda ƙarfin naushin nan take wuyan ya yi ƙara ya karye ji kake ruƙus! Kas jini ya yi tsartuwa gangar jikin ta faɗi ƙasa rikica! Nan waɗansu zaratan dakaru a fadar suka ɗauke gawar sarki Ashrum suka goge jikin da ya zuba, sannan suka tusa ƙeyar jama'ar shi izuwa kurkuku.

Sa'adda sauran sarakunan suka ga abin da ya faru ga sarki Ashrum sai cikinsu ya ɗuru ruwa domin sun san cewa a kodayaushe ɗayan su zai iya baƙuntar barzahu,

Bayan Fitinatul-Amir ya koma bisa kan karagarshi ya hakimce sai aka hango yara biyu mace da namiji sun shigo fadar sun durfafo inda karagar mulki take, ba wasu ba ne face Yaro Usaiba mai hatimin takobi tare 'yar uwarshi Hairat, lokacin da yazamana tazarar dake tsakanin su da karagar mulki bata huce taku goma kawai sai aka ga sarki Fitinatul-Amir ya miƙe tsaye tsam! Daga kan karagar mulki fuskarshi cike da annuri ya je ha tare su yaja hannayensu har izuwa kan karagar mulki suka zauna a tare.

"Wannan shi ne masu iya magana ke cewa idan rabo ya rantse... Kaico! Rashin sani wai Kaza ta kwana akan dami, haƙiƙa Fitinatul-Amir ya tafka babban kuskure da ya riƙi wannan yaro a matsayin magajin shi, shin ko bai gano cewa yaron shi ne Usaiba mai hatimin takobi SAIFUL-ZAYYAD da yake farauta dare da rana ba"

Wani daga cikin sarakunanne ya yi wannan furuci a cikin ranshi batare da ya bayyana ba,

Ana cikin wannan hali ne wani badakare ya matso daf da karagar mulki ya risina ya kwashi gaisuwa ga sarki ya ce " Ya shugabana an lissafa harajin sarki Madsur kuma tuni dakaru sun nufi Baitul-Mali domin su kai dukiyar domin haka sarki Madsur ta tawagar shi za su iya tafiya,

Koda jin wannan batu daga bakin badakaren sai Fitinatul-Amir ya gyaɗa kai alamar gamsuwa. Nan take Madsur da tawagarshi suka miƙe tsaye suka durfafi ƙofar fita daga fadar, amma koda suka zo giftawa ta gaban Fitinatul-Amir sarki Madsur ya haɗa idanu da yaro Usaiba sai suka ƙurawa juna idanu, nan take Madsur ya ji zuciyarshi ta buga da ƙarfi tsoro ya kama shi.
Jim kaɗan bayan ficewar su daga fadar sai yaro Usaiba ya dubi Fitinatul-Amir ya buɗi baki cikin alamun matuƙar damuwa ya ce "Ya abbana wannan sarki da ya fita daga wannan fadar ya shirya maka wata mummunar gadar zare ka sani cewa dukiyar da ya kawo maka a matsayin haraji bakomai ba ce face sinadaran tsafi, wadanda matsawar ka haɗa su da dukiyar ka dukkan abin da ka mallaka zai lale za ka dawo sarkin da ya fi kowa talauci a duniya"
Koda jin wannan batu daga bakin yaro Usaiba sai Fitinatul-Amir ya cika da matuƙar mamaki ainun ya dubi Usaiba ya ce "Ya aka yi kasan da hakan ya ɗana?
Usaiba ya ce "Ya abbana ka duba idan har ka tabbatar da abin da na faɗa ba gaskiya ba ne na yarda cewa na yi kuskure".

Koda jin wannan batu sai Fitinatul-Amir ya zira hannunshi a aljihunshi na riga ya ɗauko madaidaicin madubin tsafi ya shafe shi da hannun shi na hagu ya shiga gudanar da bincike, Nan take ya gano gaskiyar abin da yaro Usaiba ya faɗa game da mugun tanadin sarki Madsur.

Koda ganin wannan al'amari sai Fitinatul-Amir ya taƙarƙare ya kurwa wawan ihu da ya ɗimauta duk wata halitta dake fadar.

Mu haɗu a ƘARYA DA GASKIYA Domin jin cigaban wannan ƙayataccen labari
Daga mai ɗebe maku kewa a kullum da koyaushe.

MANSUR USMAN SUFI
Sarkin Marubutan Yaƙi
08137237071